أئمة أهل البيت رسا لة وجهاد

# IMAMAN AHLULBAYT (A.S.) SAKO DA JIHADI

## GABATARWA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin dukkan halittu.

Ya Allah Ka yi daɗin tsira ga Annabi Muhammadu da zuriyar Annabi Muhammadu kamar yadda Ka yi daɗin tsira ga Annabi Ibrahim da zuriyar Annabi Ibrahim,kuma Ka sanya albarka ga Annabi Muhammadu da zuriyar Annabi Muhammadu kamar yadda Ka sanya albarka ga Annabi Ibrahim da zuriyar Annabi Ibrahim,haƙiƙa Kai ne abin yi wa godiya Mai girma.

Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin Kai.

"Suna cika alkawari kuma suna tsoron yini wanda sharrinsa yake tarwatsuwa.

Kuma suna ciyar da abinci alhali suna son sa, ga miskini da maraya da kamammen yaƙi. Mu muna ciyar da ku ne kawai saboda Allah ba ma bukatar sakamako ko godiya daga gare ku.Mu muna jin tsoron Ubangijinmu ne game da wani yini ne na murtukewa mai tsanani.Don haka sai Allah Ya tserar da su daga sharrin wannan yini Ya kuma haɗa su annuri da kuma farin ciki".

(Surar Al-Insan aya ta 7-12)

## MATASANMU DA IMAMAN AHLULBAYT(A.S.)

Idan aka haifi yaro a gida da yanayi da yanki na addini,yayin da ya buɗe idonsa,jinsa ya fara aiki,hasashensa ya fara aiki zai ga wasu alamu na tsarkekewa da sallamawa ga Imaman Ahlul-Bayti (A.S.) daga ɓangaren iyalan gidansa da kuma guraren zamantakewarsa.

Zai gane mahaifinsa duk yayin da aka ambaci sunan Imam Ali(A.S.) ko Imam Hasan (A.S.) ko kuma wani daga cikin Imamai (A.S.) sai ya ji mahifin nasa ya biyo da wata kalmar yabawa da girmamawa gare su.

Zai ga cewa mahaifiyarsa yayin da take fuskantar wata mushkila ta zabura zuwa ga yin tawassuli da ɗaya daga cikin Imamai(A.S.) tana mai cewa:-

"Ya Ubangijina don darajar Imam Hasan, don darajar mai lamunin Aljanna "da dai sauransu.

A lokacin munasabobin tunawa da Imamai kuma kamar su, Muharram da Safar zai ga wani babban canji na gaba ɗaya da bambanci a rayuwar jama'ar gidansa ,yayin da jama'ar zamantakewa suke canjawa gaba ɗaya suke shiga cikin wani shiri na musamman da ya keɓanta da ranakun Ashura da kuma ranukun wafatin sauran ma'asumai (A.S.).Wannan zai sa shi ya kiyaye ranaku da lokutan zaman makoki,har ma ya yi sassauci a wasu al'amura nasa zuwa wasu kwanaki,hali da yanayin murna da farin ciki sun zamanto sun ɓace daga al'umma,babu ɗaurin aure,babu buki, babu faranta rai,babu murna a kwanakin watan Muharram,zai ga abin kawai da ya lulluɓe mutane shi ne baƙin ciki da juyayi duk saboda Imam Husain(A.S.) da sauran Imamai (A.S.).

Idan yaro ya girma yana lura da wannan irin yanayi sai ya haifar masa da girmamawa da tsarkakewa ga Imamai,waɗanda ya yi ta jin suanayensu a munasabobi da kuma yin musharaka a tarurrukan munasabobinsu tare da iyayensa da ma al'umma baki ɗaya.

Wannan zai dasa soyayya da ƙaunar Imamai(A.S.) a zuciyar yaro, da girmama su,ba tare da sanin wani ɓangare na rayuwarsu ba,ko kuma gudummawarsu ba, ko kuma dalilan da suka sa suka cancanci wannan girmamawar da tsarkakewar.

A cikin wannan yanayi har yaro ya girma ya shiga makaranta, ya fara shawarwari na ilimi masu tsawo, ya bi marhaloli dabam-daban da azuzuwa dabam-daban,ya karanci fannoni dabam-daban na ilimi har kuma ya kai ga marhala haɗuwa da kafofin sadarwar al'umma da suka haɗa da gidan rediyo, da jaridu, da gidan telbijin, da dish-dish,da sanin wayewar kan al'ummu da jama'u har ya sami sanin mashahuran mutane a tarihi,da masana, ya san irin gudummawar da suka bayar a rayuwar ɗan Adam da ci gabansa ta yadda har suka cancanci girmamawa da yabo.

A cikin wannan yanayi da marhala tambayoyi na iya taso masa da ke cewa :-

Ina matsayin Imamai ne a tarihi?

Ina gudummawarsu a rayuwa?

Ina abubuwan da suka aiwatar a fannin ilimi?

Ya karanta tarihi a makaranta amma bai ga wani guri ga Imamai ba a kan mumbarin Khalifanci ba, ko kuma kujera a kan karagar mulkin

shugabanci.Khalifofin da tarihi ya yi bayani game da su su ne:-Banu Umayya da Banu Abbas da Banu Usman!

Haka nan ya karanta cin nasarorin yaƙe-yaƙen musulunci,ya san mashahuran gwarzayen mayaƙa da suka ci nasara kamar su Khalid bin Walid, da Muthannaa Bin Haritha,da Sa'ad Bin Abi Waƙƙas da Ɗariƙ bin Ziyad da Musa bin Nasir da Salhuddin Ayyubi amma bai ga gudummawar Imamai ba a yaƙe-yaƙen da nasarorin da aka samu.

Haka ya karanta tarihin masana da ma'abuta bincike da ƙage-ƙage na ilimi bai ga sunan Imamai a jere da na su Pastore wanda ya ƙago maganin kashe ƙwayoyin cuta a abinci ba, ko kuma Adeson wanda ya ƙago wutar lantarki ba, ko kuma Ishaƙ Newton wanda ya gano maganaɗisun ƙasa ba, da dai sauransu.

Daga nan sai tambaya ta shigo masa yana cewa to don me muke girmama Imamai(A.S.)?

Me ya sa iyalan gidana da jama'ar al'ummata suke ba da babbar himma game da su?

Ya dace da hankali mu girmama aƙalla ɗaya daga cikin Khalifofin nan domin ya ɗauka nauyin shugabantar al'umma kuma ya yi ƙoƙarin kare amfani ga al'umma na wani lokaci,haka ya dace mu himmatu da koda ɗaya ne daga cikin mayaƙan nan da ya samar da cin nasara domin a zamaninsa an sami ƙarin faɗaɗa daular Musulunci,haka kuma mu karrama ɗaya daga cikin masu ƙage-ƙage domin ya yi hidima ga Bil-Adama.

To amma su Imamai saboda me za mu girmama su mu ɗaukaka su? Ai su ba kome ba ne illa taron ma'abuta zuhudu kawai,ma'abuta ibada,da suka zo kafin ƙarnoni uku da suka gabata suka tafiyar da rayuwarsu a salla da addu'o'i kawai sa'an nan suka mutu zamani ya ci ya cinye su ya sha ruwa a kansu.

A cikin irin wannan yanayi ne sai guguwar kokwanto da fanɗarewa ta kwashe shi a tsakanin darrusan da ya karanta da kuma tarbiyyar da aka yi masa,da koyi da wasun da yake yi duk sai su haifar masa da ruhi irin na kangarewa wanda ke ɓullowa a marhalar samartaka ya daka masa tsawar cewa ashe lokaci bai yi ba ne da za ka gane koma bayan jama'arka da raunin bi na makanta da kake yi musu,ba za ka yi bincike game da ra'ayin riƙau ɗinsu na tsarkakewa da girmama ga mutane

da a tarihi ba su da wani tasiri a da can haka nan kuma ba su da wani tasiri a halin yanzu ballantana kuma a nan gaba?

Wannan gumurzun ra’ayoyin da ke gudana a cikin tunanin matashi sai ya ruguza masa ƙarfin zuciyarsa zai ingiza shi ga kangarewa ga al’adar biyayya da koyi ga magabata har ma ya kai shi ga izgili ga al’adun addininsa.

Idan muka yi tsai da ranmu muka yi nazari za mu ga cewa tushen wannan matsala shi ne rashin kyakkyawar fahintar koyarwar addini daga ɓangaren matashin  da rashin sanin tarihin musulunci da asalinsa.A tasowarsa da yarintarsa ya ga alamu na addinin musulunci amma bai san manufofinsu ba,ya gaba bango ne bai san abinda ke cikinsa ba,ya ga shacin layi ne bai ga ainihin layinsu ba.

Shi dai ya ga jama’arsa suna girmama Imamai(A.S.) ba tare da ya san kome daga tarihin rayuwarsu ba, da gudummawar da suka bayar a rayuwa ba,in ba dan kadan da ya game ji game da yawan ibadarsu,da mu’ujizozinsu da ba za su ƙara kome ba in banda guje musu da ƙyamar su.

To a nan ne wajibin malamai zai zo, na faɗakar da matasa da fahintar da su da sanar da su game da rayuwar Imamai(A.S.),da gummawarsu a rayuwa,da salon tsarin rayuwarsu,saboda ’ya’yanmu su san darajar Imamai(A.S.) kuma su san irin gudummawa da sadaukarwar da suka yi ga bil Adam baki daya da kuma ga al’ummar musulmai a keɓance.

Wannan ɗan littafin ɗaya ne daga silsilar taƙaitattun littafa da ofishin Rasulul A’ama na ƙasar Oman ke ƙaddamarwa domin fahimtar da ’ya’yan musulmi da kuma cike giɓin tunani da sani da ke ci matasansu tuwo a ƙwarya.Domin ƙara haske ga rayuwar ja-gororin al’umma ,shugabannin shiriya amincin Allah ya tabbata gare su.

Muna fata wannan silsilar littafan za su jawo hankalin matasa masu kwaɗayi da jimirin neman iimi da fahinta da kuma samu gamsuwarsu da yardarsu.

Muna roƙon Allah Ya ba mu dacewar cimma manufa da burinmu ,da isar da saƙonmu,kuma lalle Shi mai iko ne a kan kome.

Shaykh Hasan Musa Saffar.

Maskat.20/3/1394Hijiriyya.

GUDUMMAWAR IMAMAI A RAYUWA

Shin da gaske ne cewa Imamai (A.S.) ba su kasance ba sai dai wata jam’a masu zuhudu kawai, waɗanda ba su da kome sai da salla kawai,babu wani aiki sai tasbihi kawai ba su da wani kataɓus sai addu’a kawai?

Saboda haka ba su kasance suna da gudummawa ga rayuwa ba,to mene ne dalilin samuwarsu a matsayin Imamai?

To don me suka samar da Ashura?

To  za mu iya sanin gudummawar Imamai(A.S.) a rayuwar ta wannan hanyoyin da ke biye:-

IMAMAI NAGARTA A AIKACE

Akwai wasu managartan al’amura na ’yan Adamtaka maɗaukaka da dukkan mutane ke ƙaunar su, kowace al’umma ke burinsu a zamantakewarsu, kowane mutum ke jimirin siffantuwa su shi a kan kansa,domin al’amura ne na sa’ada da kamala, kamar su yin adalci, da yin gaskiya,da kyakkyawar niyya, da sadaukarwa da yi wa jama’a hidima ko tallafa musu.

Waɗannan managartan siffofi a sakamakon darajarsu da wahalar aiwatar da su a aikace ba kasafai a kan same su fa a fagen gudanarwa a aikace,har ta kan bayyana ga mutum tamkar cewa su dai kawai a fannin koyarwa suke kawai ba a aikace ba,ko kuma kawai a tunani suke ba a aikata su,ko kuma tamkar mafarki suke ,wato aiki da su abu ne da ba zai yiwu ba,a gurin ɗan Adam mai sha’awace-sha’awace, mai son zuciya, mai kwaɗayi.

Wannan irin tunani kuwa mutum na natsuwa da shi saboda yana shirya masa yadda zai ƙetara iyakar waɗannan managartan siffofi ne,ya fita daga fagagensu, don haka sai ya ga shi a gurin ba lalle ba ne a kansa ya yi aiki da su ya aiwatar da su, kuma ba za  ya hukanta a kansa game da su ba matuƙar dai shi a imaninsa duk su a fannin koyarwa kawai suke ba na aiwatarwa a aikace ba ne da lizimtuwa da su.

To a sarari yake cewa wannan irin ra’ayi ko tunani hatsari ne mai girma ga al’umma;to amma tambaya ita ce ta yaya za mu fitar da wannan irin hatsarin ga al’umma?

Ba zai taɓa yiwuwa a gare mu ba har sai dai idan muka tabbatar wa mutum kuskuren wannan irin tunanin,muka kuma gamsar da shi game da haƙiƙanin waɗannan managartan ɗabi'un da kuma yiwuwar aiwatar da su a aikace.Hakan kuwa ba zai tabbata ba har ba tare da samun wata jama'a waɗanda za su ɗauki nauyin aiwatar da waɗannan ɗabi'un a aikace a rayuwa alhali kuma suna nan kamar sauran mutane 'yan Adam a fagen rayuwa ta kasancewarsu masu sha'awace-sha'awace da buri kamar kowa.

Samar da irin wannan jama'ar da za ta kasance mai gudanar da waɗannan ɗabi'un a aikace a tsakanin jama'a, wadda kuma za ta jure dukkan wata wahala da za ta sha a kan haka zai zamanto babban izo ne zuwa gaba a gurin sauran mutane wajen misaltuwa da su waɗannan ɗabi'un da kuma taka rawa irin tata da kuma dacewa da ita a aiwatarwarta.

A ɓangare guda kuma Allah zai hukunta mutum kuma Ya tambaye shi game da aiki da waɗannan managartan ɗabi'un,domin akwai abin koyi gare shi waɗanda suka iya aiwatarwa a aikace don haka aiwatarwa abu ne mai yiwuwa ba gagara badau ba,ba zai zamana yana da uzuri ba a gurin Allah kan kallafa masa abu da ba zai iya aikata shi ba.

Saboda haka babu makawa Allah Ya samar da wasu mutane a wannan rayuwa waɗanda zai amfani da su a wannan rayuwar domin su gudanar da waɗannan ɗabi'un a aikace.

Wannan kuma shi ne dalilin da Ya sa Allah Ya samar da Annabawa da Imamai (A.S.) wannan kuma shi aikinsu na asasi a rayuwa, Allah Ta'ala Yana cewa:-

***"Manzanni masu yin albishir kuma masu yin gargaɗi domin kada mutane su zamanto suna da hujja a kan bayan (zuwan) Manzanni***."(Surar Nisa'i aya ta 165)

Wannan kuma shi ne dalilin da ya sa ake cewa "Imami" hujjar Allah,Imamai kuma ake kiransu "Hujjojin Allah" a kan halittunSa...,hadisin da ke biye yana ƙarin haske game da haƙiƙanin wannan ala'amarin:-

Daga Imam Ja'afarus- Sadiƙ bin Imam Muhammad (A.S.) cewa:-

"Ranar Kiyama za a zo da mace kyakkyawa wadda aka jarrabe a kyawunta ,sai ta ce ya Ubangiji Ka kyauttata halittata ne har na fitinu da abinda ya auku gaare

ni,sai a zo da Maryamu (A.S.) a ce wa matar ke ce kika fi kyawu ko wannan? Mun kyautata halittarta amma ba ta fitinu ba.

Sai kuma a zo da mutum namiji kyakkyawa wanda aka fitine shi a kyawunsa,sai ya ce Ya Ubangiji Ka kyautata halittata har sai da abinda ya auku gare ni daga mata ya same ni.Daga nan sai a zo da Annabi Yusuf (A.S.) a ce wa mutumin;shin kai ne ka fi kyawu ko wannan?Haƙiƙa Mun kyautata halittarsa amma bai fitinu ba.

Sai kuma a zo da wanda bala'i ya auku gare shi, sai ya ce Ya Ubangiji Ka tsananta mini a bala'i har sai da na fitinu.Sai a zo da Annabi Ayyuba(A.S.) a c e masa shin an bala'ance fiye da wannan ne? Lalle shi an bala'ance amma bai fitintu ba.

Saboda haka aikin Imamai(A.S.)kamar aikin Annabawa ne a rayuwa wanda aiwatar da kyawawan ɗabi'u da ayyukan alheri a aikace da canja su zuwa halayyar rayuwa kome wahala kome tsanani saboda sauran mutane su yi koyi da su.Allah Ta'ala yana cewa:-

***"Haƙiƙa a Manzon Allah gare ku akwai abin koyi mai kyawu."***

(Surar Ahzab aya ta:21)

Wannan kuwa shi ne abinda Imaman Ahlul Bayt (A.S.) suka aiwatar a aikace a rayuwarsu,suka bayar da kyakkyawan misali a tarihi wajen gudanar kyawawan ayyuka da gwagwarmaya wajen ganin an yi aiki da su da sanya su a tsarin rayuwa;ga wasu daga cikin misalai a tarihi:-

1. KIMAR GASKIYA
   A karantarwa kowa yana da ra'ayin lururar yin riƙo da gaskiya tare kushe kaucew daga gareta amma kuma a ɓangare aiwatarwa a aikace shin dukkan mutane baki ɗaya a shirye suke su yi aiki da ita yayin da ta saɓa wa fa'ida da amfani kansu da manufofinsu?
   Sau da yawa mutum na gane gaskiya amma sai ya ƙi ta da gangan,saboda kawai ta ci karo da fa'idarsa;shin akwai wata gaskiya ko fa'ida ne da ta fi kujerar hukunci da karagar mulki? Wanda faɗin fagen shugabancinsa ya kama tun daga kan tsororuwar duwatsun Yeman har zuwa kan iyakokin Iran?Daga kogin Nilun Masar har zuwa gaɓar Teku matsakaiciya?
   Babu shakka fa'ida ce mai girma da shugabanci mai sanya ruɗina kai,a ce mutum ya zamanto shi ne shugaban wannan katafaren yankin yawatacce tsararre gaba da gaba da saɓawa 'yar ƙarama ga tafarkin gaskiya.

Wannan kuwa bayan kashe Khalifa Umar ɗan Haɗɗabi wanda ya assasa majalisar shawarar zaɓen khalifan al'umma bayansa, wannan majalisa ta ƙunshi mutane shida wadda ɗaya daga cikinsu shi ne Imam Ali(A.S.).
Yayin da suka taru sai Abdurrahman bin Awf ya ce-wanda shi ne shugaban majalisar-za mu yi maka mubaya'a ya kai Ali a kan aiki da littafin Allah da sunnar Manzon Allah da tsarin rayuwar manya biyu,(Abubakar da Umar);sai Imam Ali (A.S.) y ace musu:-Ku yi mini mubaya'a a kan littafin Allah da sunnar ManzonSa da kuma Ijtihadina na ra'ayina.Sai suka amince masa suka yi wa Usman bin Affan mubaya'a.Littafan tarihi sun ambata wannan al'amari kamar yadda ya zo a littafin Tabari.(Juzu'i na 3 shafi na297 bugun Darul Fikril Islamiy Berut shekara ta1410 Hijiriyya).

KIMAR TSAYUWAR DAKA DA SADAUKARWA

Haƙiƙa ƙima ce babba mai girma mai daraja, mutum ya tsaya ƙyam a kan gaskiya ba tare da damuwa da irin farashin da zai jawo masa ba...,ya yi watsi da masaye da koyarwar addininsa da kome ba, kuma ya zamanto a shirye yake ya sadaukar da dukiyarsa, da 'ya'yansa, da sahabbansa da yaransa, da iyalansa da rayuwarsa a tafarkin Allah,amma kuma wane ne wanda zai iya aiwatar da haka a aikace, ya taka wannan rawar har zuriyoyi masu zuwa a al'umma su yi koyi da shi?

Ba kowa ba ne sai Imam Husain bin Ali.

Haƙiƙa jama'a sun hana shi ruwan sha.

Sun kashe masa dukkan sahabbansa da mataimakansa

Sun yanka hatta jaririnsa da ake shayarwa.

Duk da haka ga su nan sun himmatu a kan kashe shi da kame iyalansa ko kuma ya canja ra'ayi game da yunƙurinsa ya sallama ya miƙa wuya ga hukuncin Yazidu,idan har ya yi haka to zai rayu cikin jin daɗi da annashuwa.

Sai dai shi Husaini(A.S.) ya yi watsi da wannan tayin ya ƙi canja ra'ayinsa ya ƙi ya musanya koyarwar addininsa,ya doge a gwabzawa da sadaukar da dukkan wani abu da ya mallaka yana cewa:- "A'a har abada ba na taɓa bayarwa gare ku bayar da hannu irin ta ƙasƙantacce, kuma ba zan gudu ba gujewa irin ta bayi, ni na roƙi kariyar Ubangijina da Ubangijinku Ya kange ni daga dukkan wani mai girman kai wanda bai yi imani da ranar sakamako ba.(Biharul Anwar juzu'i na 44 shafi na 191)

KIMAR KYAKKYAWAR NIYYA

Wane irin daɗi ne da shi mutum ya zamanto yana kyautatawa ga 'yan ƙasarsa,ya zama yana hidima ga raunanan al'ummarsa, mabukatan cikinsu, ba tare da neman suna ko matsayi ba hatta ma kalmar godiya gare shi.

Wane irin wahala yake da shi mutum ya tarbiyantar da kansa a kan wannan ɗabi'a ta 'yan Adamtaka mai girman daraja.

Karanta daga rayuwar Imam Ali Zainul Abidina(A.S.), ka ga yadda ya kasance yana fita cikin dare yayin da duhu ya yi tsanani mutane kuma suka yi nisa cikin sharar barcinsu,guri kuma ya yi tsit ba kowa,a wannan lokacin ne shi Imam yake fita ɗauke da buhu maƙare da kayan abinci,ko kuma salkar ruwa ko ɗaurin itace,ya nufi gidajen faƙirai da gajiyayyu,ya ƙwanƙwasa musu ƙofa idan wani ya fito daga cikin gidaan sai ya damƙa masa abinda ya kawo fuskarsa na lulluɓe domin kada a gane shi,daga nan sai ya wuce zuwa wani gidan.Idan har wani daga cikin faƙiran ya yi ƙoƙarin saninsa domin yi masa godiya, ya tambaye shi ko shi wane ne, sai ya amsa masa da cewa bawa ne daga cikin bayin Allah ka yi masa addu'a da samun gafara da rahama.

Shi Imam Zainul Abidina (A.S.) ya kasance yana da wani ɗan baffansa mai cutar da shi,Imam (A.S.) ya kasance yana zuwa gidansa da daddare yana ba shi kuɗi fuskarsa a rufe saboda haka bai san shi ko wane ne ba.Idan ya karɓa sai ya yi masa godiya kuma ya ƙara da cewa sai dai Zainul Abidina ɗan baffansa ba ya taimaka masa da kome,Imam ya kasance yana jin duk abinda yake faɗa yana shiru yana haƙuri da shi ba ya bayyana masa shi wane ne.

To yayin da shi Imam Zainul Abidina (A.S.) ya yi wafati sai alherin da miskinai,da faƙirai suka kasance suna samu ya yanke sai mutane suka gane cewa ashe shi ne ya kasance mai aikata haka.(Littafin Al-Irshad fiy ma'arifati hujajillahi alal Ibad na Malam Muhammad bin Muhammad An-Nu'uman juzu'i na 2 tahƙiƙ na mu'assasar Aalil Baytil Turaath juzu'i na 2).

To a bisa waɗannan misalan shin mun fahinci girma da muhimmanci da darajar waɗannan Imaman(A.S.).

Su su ne ainihin asalin ’yan Adamtaka waje aiwatar da ɗabi’un ƙwarai na darajar ƙoli,su ne ababan koyi ga zuriyoyi masu zuwa daga bl Adama, su hujjojin Allah ne a kan halittu baki ɗaya.

IMAMAI SHUGABANNI NA SHARI’A

Mafi muhimmancin abu da al’umma take bukatar sa shi ne shugabanci mai hikima da hukuma mai adalci,wadda za ta samar da yanayi na adalci da aminci da ’yanci ga al’umma ta kuma tafi da jama’a a bisa tafarkin ci gaba da haɓaka.

Idan aka bala’anci al’umma da shugabanci fanɗararre,da hukuma azzaluma to rayuwar wannan al’umma za ta zamanto azaba ce kawai da bala’i da ɗebe tsammani,da tsoro, da zalunci makomarta kuma babu shakka ita ce komabaya da wargajewa.

Muhimmanci wannan al’amari kuma na ƙara ƙarfi la’akari da irin abubuwan tarihi da suka auku da wahalhalun da aka sha da yanayin damuwar da aka shiga kuma ake gaba da rayuwa a cikinsa,idan har aka ci nasarar samar wa al’ummar shugabanci nagari za ta iya ƙetare wannnan tarnaƙin ta fita daga cikin wannan yanyin da dukkan alheri da cin nasara da aminci;idan kuwa ba haka ba to babu abinda ya saura sai ruɗewa da sukurkucewa da wargajewa.

Ko shakka babu cewa mafi girman rashin da ya auko wa al’umma shi ne wafatin Manzon Allah (S) a farkon shekara ta goma sha ɗaya ta hijira,domin barinsa duniya a matsayinsa na Manzo, ma’abucin saƙo, mai tarbiyyantar da al’umma ya haifar da wani babban giɓi a al’umma,domin maƙiyan wannan al’umma da wannan jaririyar daula sun kasance suna jira su samu damar da za su dira a kanta su murƙushe ta,su durƙusar da irin yunƙurin wannnan saƙon su ƙuƙƙume karagarsa. A ɗaya ɓangaren kuma ita al’ummar Musuluncin ba kai ga cikar ƙarfinta ba a sakamakon rashin ƙoshi da tarbiyyar musulunci saboda ƙuncin lokaci da ƙayyadewar yanayi da wahalar aikin kawo canji a ɗabi’a.

To mene ne abinda addinin musulunci ya tanada game da irin wannan ba zaton da ke aukowa da ke iya aukuwa a al’umma?

Mene ne abinda Manzon Allah(S) ya tanadar wa al’umma na wata makama da za ta yi riƙo da shi zuwa gaci da tsira da cin nasara?

Shin ya dace da hankali a ce addini musulunci wanda shi ne cikakken addini mai cikakkiyar koyarwa;ya dace a ce ya bar wannan al'amari a canki-canki da neman sa'a kawai?

Shin ya dace da hankali Manzon Allah (S) ya gafala game da wannan al'amarin ko kuma a ce bai damu da makomar wannan al'umma ba ta nan gaba?

Duk wanda yake karanta tarihin Musulunci nan da nan zai gane cewa abubuwa sun kasance suna aukuwa ne cikin gaggawa ba tare da saqon musulunci ya ba da wata gudummawa a kansu ba.

Don haka kafin jana'izar Manzon Allah sai Ansar,  suka hadu a wani dakin taro suna tunani game da al'amuran Musulunci nan gaba ko kuma game da rayuwarsu ta nan gaba a daula,suka kuma tuna gudummawarsu a taimaka wa Musulunci ba da goyon bayansu ga Manzon Allah (s) har wuyayensu suke leko matsayin khalifancin Musulunci, sai dai kuma masu leko kujerar ba mutane ne kadan ba ne,ba daga ƙabila ɗaya ba ne, ba daga ƙungiya ba ne, daga ƙungiyoyi biyu nebwaɗanda suke da tsohon tarihin hamayya da juna da artabu da juna wanda babu abinda ya kawo ƙarshen sai musulunci. A nan ne tsohuwar gaba ta tashi,hamayya ta fito fili tsakanin Sa'ad bin Ubadata shugaban ƙabilar Khazraj da Asid bin Hadhiyr shugaban ƙabilar Awsu.

Muhawara mai tsanani ta ɓarke tsakanin ƙabilun biyu babu abinda ya dakatar da ita sai shigowar wasu sahabbai daga cikin muhajirai, wadanda su ne Abubakar da Umar da Abu Ubaida Bin Jarrah yayin nan ne kuma muhawarar ta juya daga tsakanin Awsu da Khazraj zuwa tsakanin Ansar da Muhajiruna.Muhajirai sun bayyana  ra'ayinsu cewa haƙƙinsu ne su zamanto Khalifa ba Ansar ba.Bayan jayayya mai tsanani a ƙarshe Abubakar ya ayyana khalifa ga Umar bin Khattab da Abu Ubayda binul Jarrah,yana cewa: "Ni na amince da ɗayan waɗannan mazajen biyu a matsayin Khalifa duk wanda kuka amince da shi daga cikinsu to ku yi masa mubaya'a.Daga nan sai Umar da Abu Ubayda suka zabura suka ce a'a wallahi ba za mu ɗauki shugabanci ba a kanka ka miƙe hannunka kawai mu yi maka mubaya'a ,sai suka yi masa mubaya'a su biyun.Su kuma 'yan ƙabilar Awsu saboda kawai su raunana ɓangare abokan hamayyarsu sai suka yi gaggawar yi wa Abubakar mubaya'a, to da haka aka warware al'amarin khalifanci a wannan lokaci da ke cike mai hatsari,mai muhimmanci.(kamar yadda ya zo a littafin Tarihi na Malam Tabari juzui na 2).

Yayin da mutuwa ta zo wa Abubakar kuma sai ya kira Umar ya sanar da shi a matsayin khalifa ya ƙaddamar da shi a Matsayin khalifa bayansa ya kuma bukaci al'umma da ta goya masa baya.(Littafin Tarihin Tabari juzu'i na 2 shafi na 618).

Yayin da aka sari khalifa Umar sai ya tara mutane shida daga cikin sahabbai,waɗanda su ne kamar haka :-Ali bin Abi Talib da Usman bin Affan, Talha,Zubay bin Awwam, Sa'ad bin Abi Waƙƙas,Abdurrahman bin Awf ya ba su da cewa bayan mutuwwarsa su haɗu su zaɓi khalifa a junansu amma ra'ayi na ƙarshe ya zamanto na Abdurrahman bin Awf.

Bayan mutuwarsa sai suka taru, bayan muawara mai zafi sai Abdurrahman bin Awf ya juya ga Imam Ali (A.S.) ya ce masa :- "Zan yi maka mubaya'a a kan littafin Allah da sunnar ManzonSa da sunnar Sheikhayni( Abubakar da Umar).Sai Imam Ali(A.S.) ya ce masa, a'a sai dai a kan littafin Allah da sunnar ManzonSa da kuma ra'ayina. Abdurrahman bai yarda ba sai ya juya ga surikinsa Usman gaya masa abinda ya gaya wa Imam Ali (A.S.) cewa: zan yi maka mubaya'a a kan littafin Allah da sunnar Mazon Allah da sunnar sheikhayni (Abubakar da Umar ).Usman ya ce : na'am.Sai ya zamanto shi ne Khalifa.

An kashe Usaman bayan yunƙurin kawo canji mai tsanani...daga nan mutane suka zabura zuwa gurin Imam Ali(A.S.) suna gurin ya amince yarda ya karbi khalifanci, bayan dagewa da nacewa da sahabbai suka yi sai ya amince aka yi masa mubaya'a ya zama khalifa amma kuma sai Ummul Muminina A'i'sha da Mu'awiya suka ƙi amincewa da Khalifancinsa,Talha da Zubair ma suka warware mubaya'ar da suka yi masa wanda wannan ya jawo yaƙe-yaƙe guda uku da suka jawo hasarar rayukan ɗaruruwan dubban musulmai.

Da Imam Ali (A.S.) ya yi shahada sai mutane suka yi wa ɗansa Imam Hasan (A.S.) mubaya'a kowa ya yi in banda Mu'awiya da ya haɗa babbar rundunar yaƙi wanda hakan ya sa Imam (A.S.) ya karɓi sulhu maimakon zubar da jini da halaka rayukan musulmai,ya janye kansa daga shugabancin musulmai.

A sakamakon haka sai Mu'awiya ya zamanto shi ne khalifan Musulmai;shi kuma a ƙarshen shekarun rayuwarsa sai ya ɗora ɗansa Yazidu a kan al'ummar Musulmai a bi shi bayan ransa daga nan ne kuma khalifancin musulunci ya canja zuwa mulkin mulukiya da gado musamman ma a gurin ƙabilar Banu Umayya har zuwa loakcin da Banu Abbas suka yi musu juyin- juya hali,sun kasance suna gadar wa junansu iyaye da 'ya'ya da jikoki.

Haka tarihin musulunci ya kasance,haka al'amura masu ƙona rai suka yi ta aukuwa, shin akwai wani musulmi mai fahimtar lamura da zai amince da duk abinda ya auku a tarihi kuma ya gamsu da makomar tarihin?

Idan har wani abu mai ƙona rai mai ban takaici ya auku to mene ne abin yi ?Me ya wajaba a yi?Mene ne maganin da addini ya tanada don fuskantar irin wannan matsalar idan ta auku,wadda ta tafi da ƙarfin al'umma, ta tafi da martabarta,ta kai ta ga ramin hawiya ta komar da ita baya da faɗuwar da take ciki a halin yanzu.

Gaskiya ne cewa a halin yanzu ba za mu iya yin wani abu game da abinda ya riga ya auku, abinda ya riga ya auku ya riga ya auku amma muna da al'amura guda da muke fuskanta kamar haka:-

Ko mu yarda cewa ba zai yiwu ba na fara daga inda abin ya auku,kuma musulunci bai tanadi da musulunci ya yi na magance mushkiloli kuma ba shi da wani shiri na makomar al'umma,ko ma Manzon Allah (S)ma bai kasance yana tunani game da abinda zai auku ba bayan ya bar duniya,shin bai kasance yana da masaniya ne game da abubuwan da suka auku cewa za su auku ba ne?Idan har muka amince da haka kuwa to mun amince mun yarda cewa addininmu ya gaza ke nan shi kuma Manzonmu ya yi rashin hangen nesa,wa iyazu billahi!

Ko kuma a ɗaya ɓangaren mu ce mun  yi imani mun yarda da cewa akwai mafita da addinin Musulunci ya tanada,kuma Manzon Allh(S) ya yi nazari da tunani a kan abinda zai je ya zo ya yi tunani game da makomar al'ummarsa, da saƙonsa da amincin al'ummarsa kuma ya yi shiri ya dauki matakai da suka dace sai dai kuma abinda ya auku sakamakon munana tawili ne da fassara ga matakan da ya tsara;don haka abinda auku kuskure tare da taimakawar abinda yanayi ya haifar,a sakamakon haka abinda ya kamata mu yi shi ne mu sanya hannunmu a kan ainihn gurin da kuskuren ya auku,wato rashin sani da kuma kuskure aiwatar da koyarwar addini daga ɓangaren masu ja-goranci da shugabanci.

To a halin yanzu mene ne abin yi,mene badalin da addinin Musulunci ya tanada? Wace mafita Mazon Allah (S) ya tanada dangane da al'amarin Khalifanci da shugabanci?

Mu mun yi imani cewa tun farkon kira Manzon Allah (S), a bisa shiryarwar Mahalicci, ya yi aikin tarbiyyantar da magaji wanda ya dace da ja-gorantar al'umma idan har shi Manzo (S) ba ya nan,wanda zai iya cike giɓin idan Manzon

Allah ba ya nan,wannan kuwa shi ne Ali bin Abi Talib(A.S.) ɗan baffan shi Manzon Allah (S)ɗin, mijin ’yarsa Fatima (A.S.) wanda ya rene shi tun yana yaro ƙarami, ya tarbiyyantar, ya saita tunaninsa a bisa manufar da yake so,ya kyautata ɗabi’unsa, Imam Ali (A.S.) ya ba da bayanin wannan himmatuwa ta musamman kamar yadda yake cewa:-

"وقد علمتم موضعي من رسول الله(ص) بالقرابةالقرابة والمنزلة الخصيصة وضعني فيي حجره أنا ولد يضمني الى صدره و يكنفني في فراشه ويمسني جسده..................................................

“Haƙiƙa kun san matsayina daManzon Allah na dangantakar kusaci da da matsayi keɓatacce, ya sanya ni a cinyarsa ina ƙarami yana rungume ni a ƙirjinsa ya lulluɓe ni a mayafinsa ya shafa mini jikinsagumin jikinsa ya tsantsame a jikina kuma ya kasance yana tauna abu ya sanya mini in zuƙe shi.Bai taɓa samu na ina maƙaryaci ba a magana ko kuma mai kwaɓa al’amura ba a aiki.Haƙiƙa Allah Ya haɗa shi da wani Mala’ika mafi girma tun lokacin da aka yaye shi, yana tafi da shi tafarkin kwawan ɗabi’un ƙwarai baki ɗaya,dare da rana.Ni kuma na kasance ina bin sa bi irin na ɗan yaye da ke bin uwarsa,kowace rana yana ƙara ɗaukaka ni a ɗabi’unsa yana yi mini umarni da koyi da shi kuma ya kasance yana zama kusa da kogon Hira kowace shekara,ina ganinsa kuma babu wani mai ganin sa sai ni.A wancan lokacin gida bai haɗa gida da ya ƙunshi mutane masu bin musulunci in ba Manzon Allah da Khadija da ni na ukunsu, ina ganin hasken wahayi kuma in shaƙar ƙamshin Annabci.”

Kuma haƙiƙa na ji kururuwar Sheɗan yayin da wahayi ya sauka gare shi(S) sai na ce masa : “Ya Manzon Allah wannan kururuwar mene ne? Sai ya c wannan Sheɗan ne ya ɗebe tsammani daga bauta masa,haƙiƙa kai kana jin abinda nake ji kana ganin abinda nake gani amma kai ba Annabi ba ne amma kai waziri ne mataimaki ne kuma haƙiƙa kai kana kan alheri[1]

Nisa’i ya ruwaito daga Imam Ali (A.S.) ya ce : “Ni na kasance ina da matsaya a gurin Manzon Allah wadda babu wani daga cikin halittu da ya kasance yana da ita in ba ni ba,na kasance ina zuwa gare kowace asuba in ce Assalamu alayka ya

---

[1] Nahjul Balagha juzu’i na 2 shafi na157 Ibin Abil Hadid binciken Abul Fadhli Ibrahim juzu’i na13,bugu na farko shekara ta 1378 hijiriyya(Berut Darul ihyakutubul Arabiyya Isa Al-Halbiy,Taħkiƙ Mahammad Abul Fdhli Ibrahim shafi na 197.

Annabin Allah,idan ya yi jinkiri sai in koma gurin iyalina,idan kuwa bai yi ba sai in shiga gurinsa”.[2]

Haka nan a wani lokacin kuma ya ce:- “Ya kasance gareni lokutan shiga gurin Manzon Allah sau biyu:lokacin shiga da daddare da  kuma lokacin shiga da rana”.

A wani lokacin kuma ya ce:- علمني رسول الله ألف باب كل باب يفتح ألف باب

“Manzon Allah ya koya babi dubu na ilimi kuma kowane babi  ya bude wata dubu .”

Da wannan irin tarbiyyantarwar ne Imam Ali (A.S.)ya zamanto ya dace da shugabantar al’umma,domin ci gaba da tarbiyyantar da ita irin tarbiyyar da ta dace da yardar ubangiji da koyarwar musulunci.

Haƙiƙa Manzon Allah (S) ya bayyana dacewarsa da khalifanci ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba a gurare daban-dabam;tun daga kan lokacin gargaɗi ga dangi makusata inda ya ce masa:-

“Kai Ɗan’uwana ne kuma wasiyyina kuma khalifana bayana”. Har zuwa ƙarƙarewa da mashahurin abinda ya auku a Ghadir Khum yayin da Manzon Allah (S) ya yi wa Musulmai waɗanda suka je aikin haji na ban kwana  da shi  huɗuba yana cewa:-“ Shin ba ni ne mafi daraja ba ga muminai a kansu fiye da su kansu .Suka ce,haƙiƙa haka ne;sai ya ce alhali yana riƙe da hannun Ali :Duk wanda ni shugabansa ne to ga Ali shi ma shugabansa ne,Ya Allah Ka so wanda ya so shi Kuma ka ƙi wanda ya ƙi shi Ka taimaki duk wanda taimake shi,Ka bar duk wanda ya bar shi,kuma ka jujjuya gaskiya tare da shi duk inda ya juya”.

Haka nan kuma shi Imam (A.S.) ya himmatu da tarbiyyantar da ’ya’yansa Hasan da Husaini domin ya saita su kan shugabanci na nan gaba.

Imam Husain ma haka ya yi ga ɗansa Ali Zainul Abidin.Shi kuma Imam Zainul Abidina ya himmatu da tarbiyyar ɗansa Baƙir,haka dai aka yi ta yi har zuwa kan Imamul Hujja,Imami na goma sha biyu.

Wannan kuma ba wai yana nufin  mun yi imani da gado a shugabanci ba ne domin shi gado a shugabanci bai dace da tsarin Imamanci ba,idan kuwa da ba haka ba ne to me ya sa Imamancin daga kan Imam Husain (A.S.) alhali ɗan’uwansa

---

[2] Abu Abdurrahman Shu’aibn Nisa’i .Sunanul Kubraajuzu’i na farko 1411hijiriyya(Berut Darul kutubil ilmiyya shafi na 360.

Muhammad Bin Hanafiyya yana nan? Ko kuma don me daga Imam Ja'afarus Sadiƙ (A.S.) sai Imam Musa Kazim (A.S.) ba babban ɗan'uwansa Abdullah ko Isma'il ba?

Imamanci zaɓi ne daga Allah kawai,tare kuma da tarbiyyantarwa da taryartarwa ta musamman ga su Imaman.

Allah Ya so ne kawai Ya so Ya nufa cewa Imanmanci ya ɓullo daga gidan mafi ɗaukaka,wato gidan Manzon Allah (S) kuma Ya nufi kowane Imam daga Imam ne da aka haife ne daga Imami kuma yana nan domin Ya zamanto shi ya jiɓinci tarbiyyantar da shi da shiryar da shi ta hanya mafi dacewa.

A nan babu makawa mu yi ta'akidin cewa ainihin wajibin Imamai a bisa ɗabi'a shi ne jagorantar al'umma ta hanyar hikima da fahimta,su su shigar da al'umma hanyar samun ci gaba da kuma kaiwa ga sa'ada, tare da kore wa al'ummar mushkiloli da rikice-rikice;sai dai kuma abin ban takaici da baƙin ciki shi ne ba ba wa waɗannan Imaman damar aiwatar da wajibinsu ba da gabatar da saƙonsu na jagorantar al'umma ba.

Idan da yanayi ya haifar dama ta samu sun kai ga karagar ja-gorantar wannan al'umma to da tarihi da ake da shi ba irin na yau da ake da shi ba ne da halin da al'umma ke ciki ba irin wanda take ciki yanzu ba ne.

IMAMAI DA WAJIBIN SAKON MUSULUNCI

Addinin Musulunci saƙo ne na dindindin wanda Allah Ya tanade shi tsararre cikakke ga bil Adama har zuwa ƙarshen rayuwa.

Wannan saƙo na Musulunci kammalalle wanda ke sanya ƙamshin rayuwar ɗan Adam, wanda ya tsara dukkan wani motsi nasa, yake sanya masa matsayi da ra'ayin siyasa da na tattalin arziki da da na zamantakewa, shi wannan saƙon ba ya bukatar marja'i ne,madogara da zai koma gare shi wanda zai ɗauki nauyin yaɗa shi,ya fahimtar da saƙonsa, ya kuma kare shi daga maƙiyansa daga waje ya kange shi daga fanɗarwa da gurɓatarwa?

Annabi(S) shi ne ya kasance garkuwa ga Musulunci da yake ɗaukar duk wannan nauyin yayin rayuwarsa, shi ne mai lura da yaɗa da'awa, shi ne mai bayar da bayani game da manufar saƙon da koyarwarsa da cikakkiyar ma'anar kariya da kangiya ga shi wannan saƙon.

To amma tambaya ita ce shin bayan Annabi (S) wane kuma zai dauki wannan nauyin ? Wane ne zai sanya wannan alkyabbar jagorancin?

Addinin Musulunci ya fara yaƙar ƙasashe daban-dabam a al'adunsu,da zamantakewarsu,da abubuwan da suke riƙo da su na iyaye da kakanu kuma wannan shi kansa yana ɗauke da hatsari na yiwuwar sulalowar al'adunsu zuwa cikin al'ummar Musulmi.

Su kuwa maƙiyan Musulunci ba za su yi jinkiri ba wajen ɓullo da wasu shubuhohi da shakkoki a gaban wannan sabon saƙon ba.Kuma al'ummar Musulunci kuma ba ta rabuwa da masu yin zagon ƙasa daga cikinta masu ƙoƙarin karkatar da akalarta kamar yadda ya auku a saƙonnin da suka gabata.

Sama da wannan kuma shi ne Musulmai za su karo da sababbin al'amura nan gaba waɗanda Alƙura'ani bai kawo nassosi game da su ba kuma Manzon Allah (S) bai yi magana game da su filla-filla ba, to su yaya za a yi da su kuma yaya za a san ra'ayin Musulunci game da su?

Zai iya zuwa cikin tunanin mutane cewa ai Sahabbai da Malaman al'umma na iya ɗaukar wannan nauyin bayan kasancewarsu sun rayu tare da Manzon Allah (S) sun ji daga gare shi sun kiyaye.

Amma idan muka yi la'akari da ƙarancin lokacin da sahabban suka kasance tare da Manzon Allah,wanda bai wuce tsawon ƙarni ɗaya ba (sekaru goma)wato wannan lokacin da aka assasa al'ummar Musulunci a Madina wadda kuma a cikinta aka sassaukar da shari'o'i da tsare-tsare na Musulunci,har ila yau kuma muka lura iri tarin matsaloli ƙalu balen da dinga dumfaro wannan al'umma da suka kasane suna ɗauke mafi yawan tsawon lokacin wannan sabuwar al'ummar to da mun fahinci cewa a cikin wannan gajeren lokaci da irin yanayin ba su bayar da dama ga sahabbai har su iya cikakkiyar masaniya game da wannan saƙo ba,da koyarwarsa da hukunce-hukuncensa,wannan kuma ba tare da ambata abubuwa sababbi da za su iya aukuwa nan gaba.

Kana iya fahimtar haka da jin haƙiƙanin wannan ala'amari ta hanyar karantawa da nazarin wannan al'amari ta hanyar nazarin saɓanin da ya auku a tsakanin sahabbai wajen aiwatar da hukunce –hukunce shari'a hatta ma a kan ibadar ma kanta bayan Manzo (S) ya bar duniya kai tsaye ,alal misali :-

“Ɗahhawiy ya ruwaito daga Ibrahim ya ce : “An karɓi ran Manzon Allah (S) mutane suna da saɓani a kan sau nawa ne adadin kabbara da ake yi a sallar jana’iza ,ba za ka so ka ji wani ya ce na ji Manzon Allah (S) ya ce yana yin kabbara sau bakwai,wani kuma ya ce na ji Manzon Allah(S) yana yin kabbara sau biyar, wani kuma ya ce na ji Manzon Allah(S) yana yin kabbara sau huɗu.Sun sassaɓa a kan haka har zuwa lokacin da Abubukar ya rasu ya bar duniya.

Tarihin rayuwar sahabbai cike yake da mshkiloli game da yadda suka fuskanci al’a muran da za a nan gaba. Alal misali sunnar Khalifa Abubkar da Umar ita ce idan wani abu ya auku wanda ba su da wata mafita a kai sai su taro masana, idan aka sami wani hadisin Annabi dangane da amsa sai su yi riƙo da shi idan kuwa babu to sai su yi ijtihadi,idan kuwa suka ijtihadi kuma suka amince fbaki ɗaya to wannan ya zamanto Ijma’i kuma ya wajaba a yi aiki da shi,idan kuwa suka yi ijtihadi amma ba su haɗu a kan abu guda ba to sai shugaba ya ba da ra’ayi to ya wajaba a yi biyayya gare shi, idan kuma ya zamanto bai ba da ra’ayi ba to sai kowa ya yi aiki da abinda ijtihadinsa ya nuna masa.

Sunnar Khalifofi biyu na ɗaya da na biyu haka ta kasance, haka nan kuma matukar ba ya kai har ga khalifa ba ne to duk sauran shugabanni haka sukakasance suna aikatwa a yankunansu.

Kana iya suranta cewa wannan ijtihadi da sahabbai suka yi ya yi daidai kuma sahihiyar hanya ce ta warware mushkilolin,sai dai kuma ta yaya za tabbatar mu kuma amince cewa ya yi daidai da abinda Allah Yake so,ya yi daidai da shari’a ɗari bisa ɗari.

Yin kuskure abu ne na ɗabi’ar yin ijtihadi, kuma idan akwai kuskure mai ijtihaddin yana da uzuri a gurin Allah amma duk da haka ai bai kai mu ga haƙiƙanin ingantaccen hukuncin da Allah Ya shar’anta mana ba.

Na Biyu:

Yayin da addini ya kasance bai ayyana wani marja’i takamaimai da za a koma gare shi da amsa tambayoyi, wanda al’umma za ta koma gare shi kuma a yi biyayya gare shi,al’umma ta kasance ta natsu da ra’ayinsa ba shin rashin haka ya haifar da sassaɓawar ra’ayoyi ba da saɓani a ijtihadi ba?

Idan ba a yi haka ba to ra’ayin wane ɗaya al’umma za ta bi?Wane ne zai iya lamuncewa cewa wannan saɓanin ra’ayin ba zai zamanto musabbabin rarraba kan

al’umma ba, ba zai kai ga hamayya da husuma ba kamar yadda muke gani a aikace a wannan zamani?Ta yadda mazhabobi suka yawaita ta yadda ra’ayoyi suka zamanto suna cin karo da juna,wani sashe na kafirta wani sashe, wasu na fasiƙantar da wasu, wasu ma fitar da wasu daga addini.

To ya bayyana a sarari garemu cewa warware matsaloli ta hanyar lumana da ruwan sanyi,tare da samar da waraka mai ɗorewa da ra’ayi na gaskiya mai kawo haɗin kan al’umma na bukatar malami wanda zai ɗauki wannan nauyin,wanda zai iya fahimtar da al’umma ya wayar mata da kai,ya iya bayyana raa’yin musulunci a sababbin al’amura masu aukuwa,ya iya kare addini daga harin maƙiya da ’yan malƙodiyo.

Wannam shi ne tsari wanda ya dace da aikin Imamai (A.S.) tsarkaka waɗanda muke da imanin cewa Ya tanade su ne domin yin haka ManzonSa kuma ya sanar da su don ɗaukar wannan nauyin kamar ya zo a hadisai a bisa ittifaƙin malamai cewa ya ce:- “Ni mai barin abubuwa guda biyu masu nauyi ne a tsakaninku,ɗayansu ya fi ɗayan girma ,littafin Allah wanda yake abin miƙowa ne daga sama zuwa ƙasa da kuma zuriyata matanen gidana,kuma haƙiƙa su ba sa taɓa rabuwa har sun iske ne a tabkin Alkausara”.

A wata ruwayar kuma ya zo cewa:-

“Haƙiƙa ni mai bar muku abu ne da idan kuka yi riƙo da shi ba za ku taɓa ɓacewa ba bayana har abada,ɗayansu ya fi ɗayan girma:littafin Allah wanda igiya ce abar miƙowa daga sama zuwa ƙasa,da kuma zuriyata mutanen gidana domin su biyun ba za su taɓa rabuwa ba har su iske ni a tabkin alkausara,saboda haka ku lura da yadda za ku wakilce ni a kan su biyun nan.”

To tunda yanayi bai ba da dama ba ga Ahlul-Bayt (A.S.) don aiwatar da aikinsu da ya ɗoru na ja-gorancin al’umma da shiryar da isar da saƙo da ba shi kariya don haka sai suka kasance suna amfani da wata damar da suka samu suna cin gajiyar duk wata dama da suka samu wajen bayyana wa mutane muhimman ayyukan da suka ɗoru a kansu, su koyar da musulunci.A nan za mu kawo wasu misalai da ke ire-iren gudummawar waɗannan Imamai(A.S.)kamar haka:-

AL’AMARIN SHARI’A

Wata matashiya budurwa mai kame kai ta kare budurcinta da kamun kai da amana da mutunci tare da riƙo da koyarwar Musulunci har zuwa lokacin da wani

daga cikin Musulmai ya aure ta.Cikin ikon Allah da yarjewarSa sai ta haihu bayan wata shida da ’yan kwanaki da aurenta alhali kuma alhali kuwa a bisa ɗabi’a da sanin mutane mace kan haihu ne bayan wata tara, to wannan ya sa wannan matashiya ta zamanto a bar tuhuma da zargi da yin tir da ita a harsunan mutane masu bibiyar laifukan wasu wannan kuwa ya sa mijinta ala tilas ya kai al’amarin gurin Khalifa Umar bin Khaɗɗab.

Sai dai kuma shi ma kansa Umar ɗin fahimtarsa irin ta sauran mutane ce kan cewa tsawon lokacin ciki wata tara ne don haka bai yi wani jinkiri ba wajen yanke mata haddin zina.Nan da nan suka yi wuf da ita a bisa hukuncin Umar aka tafi wajen zartar da haddi zina a kanta,ran wannan matashiya ya yi dubu ya ɓaci zuciyarta tana ta ƙuna tana raɗaɗi tana tambayar kanta cewa ta yaya Allah zai ƙaddara mata haihuwa a cikin watanni shida kuma a yi mata hukuncin zina? Ta yaya za a warware ƙudarar Allah a halittunSa?

Shin wannan hukyncin kuwa daidai ne ko kuwa dai Khalifa ne ya yi kuskure? To idan kuskure ne wanene zai kare mutane ya kuɓutar da su daga wannan kuskuren?

Da Allah Ta’ala Ya nufi tserar da wannan matashiya da kuma tabbatar da rashin laifinta da adalcinSa sai Ya nufi Imam Ali (A.S.) da wucewa ta gurin inda ya ga mutane sun taru suna kallon yadda za a zartar sa haddi kanta.Sai Imam (A.S.) ya tambaya ko menene yake faruwa;sai aka ce masa ai wata matshiya da ta haihuwa alhali kuwa ba ta fi watanni shida ba da yin aure ba .

Sai Imam ta katse su ya ce to menene matsaala a hakan?

Suka ce masa ai wannan ya nuna cewa ta yi zina Kenan kafin aurenta da wata uku don haka ne ma Khalifa ya yi hukunci da a yi mata haddi.

Sai ya musu ku dakata har sai na je na dawo. Daga nan sai Imam (A.S.)ya gaggauta zuwa gurin Khalifa Umar ya ce masa menene madogararsa na yanke mata haddin . Sai Umar ya ce saboda tsawon ciki ai ba zai yiwu ya zamanto wata shida ba. Sai Imam (A. S.)ya ce masa ai Alƙura’ani ya tabbatar da cewa mafi ƙarancin tsawon lokacin haihuwa wata shida ne,sai Umar ya ce: A ina hakan yake a Alkura’ani?

Sai Imam (A.S.) ya karanto masa Allah Yana cewa:-

(surar Lukman:14)

(surar Ahaƙaf aya ta 223)

Saboda haka idan muka rage lokacin shayarwa, wato watanni 24 daga lokacin cikai haɗe da na shayarwa wato watanni 36 zai zamanto wata shida kadai shi ne ya saura a matsayin lokacin ciki shi kaɗai ɗinsa.

Da Khalifa Umar ya ji haka sai ya tsaya a kan wannan ra'ayin ya kuma furta mashahuriyar maganarsa ɗinnan da ya ce:-

"Idan da ba domin Ali ba da Umar ya halaka".Sai kuma ya sa aka salami wannan matashiyar.

BABU KAME BAKI GA  ZALUNCI

A sakamakon danniya da  gallazawa da barazana sai aka shiga halin kame baki da sallamawa ga zalunci da fasadi da ɓarnar da ke aukuwa a al'umma.Su kuma masu goyon bayan matsayi irin wannan hali karaya suka sanya masa launi na addini tare ƙago dalilai da hujjoji na shari'a suka ba da fassarori da fatawoyi kan yi shiru da lamɓo da sallamawa ga halin da ake ciki tare da kore duk wani ƙoƙari ko wani yunƙurin kawo canji, suka kambama wannan matsayi nasu da wasu maganganu da imma isnadansu ba su da inganci ko kuma an munana musu fassara tare kururutawa da yayata waɗannan ruwayoyi da aiwatar da su.

Hatsari da illar wannan matsayi kuwa ga musulunci ba a ɓoye yake ba, domin wannan na ƙarfafa aukuwar fasadi da ci gaban zalunci da fanɗarewa.

A cikin irin wannan hali ne kuma shugabanni Imamai(A.S.)daga suka tsayuwa ƙyam don aiwatar da wajibin da ya ɗoru a kansu na kariya ga saƙo da yaƙi da wannan irin matsayi na miƙa wuya da kauce hanya su bayyana ra'ayin musulunci na kawo juyi da yin tir game da yin shiru game da taɓarɓarewar yanayi da fassara cewa yin shiru a gaban fasadi tamkar haɗaka a aikace kuma a laifi.

Haƙiƙa Imam Husain (A.S.) ya aiwatar da wannan a aikace yayin da ya yi yunƙurinsa na fito na fito da zalunci ya bayyana koyarwar addinin Musulunci game da fasadi da ɓarna inda ya kawo hadisi daga Manzon Allah (S) inda yake cewa:-

"Duk wanda ya  ga wani shugaba azzalumi yana halatta abinda Allah Ya haramta,yana warware alkawarin, yana saɓa wa sunnar Manzon Allah,yana aiki

cikin bayin Allah da saɓo da zalunci amma bai canja ba a aikace ko kuma da magana to yana ga Allah Ya shigar da shimashigarsa[3]".

Wannan shi ne wani nau'i na gudummawar Imamai a rayuwarsu kuma shi ne mafi girma kuma mafi muhimmanci, wato aikin kawo canjin yanayin siyasa da zamantakewa kazalika shi ne mafi girman barazanar fanɗarwa da wargajewa.

Ko shakka babu Imamai (A.S.) sun ɗauki wannan nauyi da ya ɗoru a kansu a matsayin wajibi da suka sadaukar da kome nasu wajen aiwatar da shi,hatta jininsu da rayuwarsu.

KA'IDAR ADDINI ITA CE MA'AUNI

Haƙiƙa addinin Musulunci ya tarbiyyantar da al'umma a bisa fahimtar al'umara sosai,daga cikin abubuwan da ya himmatu da shi kuma ya dasa su a zukatan musulmi ita ce cewa ƙa'ida ta zamanto ita c ma'aunin tantance duk wani al'amari ko motsi ko aiki ko hukunci da mutum zai yi da sunan musulunci,hakanan su mutane a kan kansu ba su da wata martaba ko daraja sai dai gwargwadon riƙonsu da ƙa'idojin da musuluncin ya gindaya;saboda haka duk wanda ya saɓa wa waɗannan ƙa'idoji kauce hanya to lalle ne a nusar da shi ya dawo hanya a fahimtar da shi kuskurensa ko shi wanene kuwa koda wace daraja ya kai kuwa.

Al'umma ta kasance tana bin waɗannan ƙa'idoji tana aiki da su hatta a kan khalifofi masu shugabantar al'umma.

A zamanin Khalifa Umar yayin da ya so ya kallafa wa mutane wani hukunci na kuskure sai wata mata ta yi farat ta sha gabansa ta ƙalubalance shi da hujja daga Alƙura'ani mai girma ba tare da ta yi ƙasa a gwiwa ba, inda hakan ya tilasta wa Khalifan janye ra'ayinsa tare da yin furuci da kuskurensa.

Malam Abdurrazzaƙ ya ce: "Yayin da Umar ya ce kada ku zurfafa wajen biyan sadakin mata, sai wata mata ta ce masa: "Ya Umar ba ka da wanna ikon haƙiƙa Allah Yana cewa: Kuma kun ba su dukiya mai yawa..." Sai Umar ya ce:mata ta ja da Umar kuma ta rinjaye shi".[4]

---

[3] Tarihit Tabari juzu'i na 4 shafi na 304.

[4] Fathul Bariy sharhu Sahih Bukhariy Juzu'i na 9 shafi na 382 bugu na huɗu bugun Berut maɗaba'a Daru Ihya'u Turathul Arabiy da Kanzul Ummal juzu'i na 16 shafi na 538

Abu Zarril Ghifariy kuwa duk da talaucinsa da ƙanƙan da kansa , yayin da ya ga an fanɗare a zamanin Khalifa Usman ana ta facaka da dukiyar baitulmali sam zuciyarsa ba ta yarje masa da ya yi gum da bakinsa ya yi shiru ba,a'a yunƙuri ya yi yana nuna rashin amincewarsa yana kira zuwa ga kawo gyaran halina da ake ciki.

To samun irin mutane masu irin wannan zuciya ta kawo gyara a cikin al'umma shi ne lamunin amincin ƙa'idojin wannan al'umma da tsayuwar dakanta da makomarta.

Sai dai kuma bayan wani ɗan gajeren lokaci sai musulunci ya yaɗu wasu ɓangarori na musulmai masu son rai suka yi ƙoƙarin yin watsi da aikin wannan ƙa'idar mai matuƙar muhimmanci ta ƙoƙarin kawo gyaran domin kawai su ba wa wasu daraja da ƙima su a kan kansu da kuma ba su damar kawo canje-canje ba tare da wasu sharuɗu ko ƙa'idoji ba,a sakamakon haka sai suka zamanto su waɗannan wasu mutanen sun fi ƙarfinbin doka da oda ayyuka da zartarwarsu kuma su ka zamanto su sharuɗa su ne ma'auni.

Daga irin ƙoƙari canjawar ne aka kai ga tsarkakewa da girmamawa ga dukkan sahabbai da suka rayu da Manzon Allah(S) da halatta duk abinda suka aiwatar ko suka aikata, tare da ƙago wasu hadisai na ƙarya aka kuma danganta su ga Manzon Allah(S),kamar hadisin ƙaryan nan da ke cewa:-

"Lalle haƙiƙa sahabbaina kamar misalin taurari suke kowanne daga cikinsu kuka yi riƙo da maganarsa to kun shiriya".

Dangane da wannan hadisin Malam Muhammad Nasiruddin Albani ya ce : Wannan haƙiƙa ƙagagge ne; kuma ya kawo daga Ibin Hazmi maganarsa cewa:(6/83) "Ya bayyana a sarari cewa cewa wannan ruwayar ba za ta tabbata ba a asali,bil hasali ma dai ƙarya ce,domin Allah Ta'ala Yana cewa inda Yake siffanta AnnabinSa Yana cewa: "Kuma ba ya magana a bisa son rai.Ba kome ba ne sai dai wahayi ne da ake saukarwa." To idan har maganarsa a shari'a gaskiya ne kuma wajibi ne to kuwa babu tantama daga Allah yakeabin kuwa da ya kasance daga Allah yake to ba za a sami saɓani a cikinsa ba saboda faɗinSa Ta'ala :-

"Idan da ya kasance daga wanin Allah yake to da sun sami saɓani da yawa a cikinsa".

Allah kuma Ya hana rarraba da sassaɓawa a cikin faɗinSa cewa: "Kuma kada ku yi jayayya.Saboda haka abu wanda yake ba zai taɓa yiwuwa ba Manzon Allah (S) ya

ba da umarnin  a bi kowane mai magana a cikinsu domin wani na iya halatta abu waninsa kuma ya haramta shi,idan da ya kasance haka kuwa to da sayar da giya ya zamanto halal a koyi da Samrata bin Jundabi,da cin BURDI ya zamanto halal ga mai azumi a koyi da Abi Ɗalha koyi da waninsu kuma da ya zamanto haramun,haka nan da barin wanka saboda IKSALI ya zamanto wajibi a koyi da Ali,Usman,Ɗalha,da Abayyu bin Ka'ab, koyi da A'isha kuma da Ibin Umar a kan haka.Domin duk waɗannan an ruwaito su a gurinmu da ingantattun isnadai."

Daga  nan sai ya tsawaita wajen kawo bayani game da wasu ra'ayoyi da suka zo daga Sahabbai da suka kuskure wa suuna a ra'ayoyin nasu,wasunsu tun zamanin Manzo(S) yana raye wasunsu kuma bayan ya bar duniya.Daga bisani sai ya ce to ta yaya zai halatta a yi taƙalidi da mutane waɗanda suke yin kuskure wani lokaci wani lokacin kuma su yi daidai?[5]

To idan har wannn hadisi ya inganta to lalle ya dace a aiwatar da shi ne a kan sahabbai masu riƙo da ƙa'idojin da Annabi (S) ya gindaya ne domin daraja da ƙimarsu sun same ta a sakamakon haka.Amma  waɗanda suka waske suka auka cikin fanɗarewa da bin fa'idarsu kawai to ba zai yiwu a aiwatar da wannan hadisin a kansu ba don kawai su zamanto abin koyi ga zuriya masu zuwa ba da dalillin cewa sun rayu na 'yan kwanaki tare da Manzon Allah(S).

Haƙiƙa Imamai sun tsaya ƙyam wajen bankaɗo ire-iren waɗannan kura-kuren da ƙa'idoji da koyarwa na kuskure da suka tattara a cikin Musulunci.Kamar yadda ya zo a maganar  Imam Ali (A.S.) inda yake cewa:-

''Haƙiƙa ita gaskiya ba sanin ta ta dubi ga mazaje ka san gaskiya kawai to za ka gane su  wane ne ma'abutanta ".[6]

Yayin da wasu daga cikin Sahabbai suka zamanto tarnaƙi ga kawo gyaran da Imam yake ƙoƙarin ga al'umma yake yi a lokacin da ya zamanto Khalifa to nan ne ya zamanto masa babu makawa ya yaƙe su,ya tsaftace su,ya gyara su idan suka doge a yunƙurinsu faɗa da shugabanci na shari''a duk kuwa da cewa sun kasance daga cikin manyan sahabbai a da suka kasance suna tare da Manzon Allah(S) a da can.

---

[5] Littafin Silsilatul Ahadisid dha'ifah na Muhammad Nasiruddin Albaniy juzu'i na farko hadisi 61 bugu na1 shekara ta1993 Riyadh MaktabatulMa'aarif shafi na 149-151.
[6] Tafsrin At-tibyan na Abu Ja'afar Aɗ-Ɗusiy  juzu'i na1 bugun shekara ta 1409,Maktabul I'ilamul Isllamiy tahƙiƙ Ahmad Habib Kasir Al-Amuliy shafi na190.

Da waɗannan bayanai ne muka fahinci matsayin Imamai (A.S.)da wajibinsu a al’umma na aiwatar da musulunci a aikace, da jagoranci a shari’a  da kare ta da kuma sauke wajibin da ya ɗoru a kansu saƙon Musulunci.

SIFFOFIN IMAMAI

Imamanci matsayi ne mai muhimmanci ,aiki ne mai nauyi wanda rayuwar al’umma ta ta’ llaƙa da shi,da makomar saƙon addinin musulunci.Shin kowane musulmi game gari  zai iya ɗaukar alkyabbar wannan shugabancin  ya sanya?.Ko kuwa akwai wasu mutane na musamm masu siffofin da suka dace na musamman? Waɗanda duk wanda zai ɗauki wannan nauyi lalle ne ya zamanto ya cika su waɗannan sifofin tukuna kafin ya ɗauki wannan wajibin domin ya iya jan al’ummar zuwa ga tsira da sa’ada?

A nan mun zo wurin da ya dace mu kawo waɗannan sifofi kamar yadda yake a koyarwar musulunci da kuma yadda zahirin rayuwar Imamai(A.S.) ya nuna.

ISMA SHARAƊIN JAGORANCI

Abinda Isma ke nufi shi ne cikakken riƙo da addini a koyaushe da kuma samun gaskiya daidai a kowane al’amari.

A bisa wannan ma’ana isma babu makawa ta tabbata a jagoranci domin jagora shi ne abin tambaya

1. Wajen bayyana hukunce-hukuncen addini,da yaɗawa da isar da hukunce-hukuncen shari’a zuwa ko’ina tare kuma aiwatarwa a aikace da kuma kare shari’a a kodayaushe.Idan ba haka ba kuwa to ta yaya mutum za su amince da jagora wanda ake ganowa cewa ya fanɗare ya saɓa wa abinda yake kira zuwa gare sh?

2.A ƙaddare jagora lalle ne ya zamanto abin koyi ga mutane, ayyukansa da maganganunsa da matsayensa duk hujja ne a kan mutane saboda haka kuskurensa ko fanɗarewarsa na iya kai al’umma baki ɗayanta zuwa ga halaka da azabar hawuya.

3.Idan aikata saɓo ko fanɗarewa sun halatta ga ɗaiɗaikun mutane a al’umma to wannan yana iyakacin da’irar ɗaiɗaiku ne kuma yana ƙarƙashin la’akarin doka da

oda amma idan daga har saɓo ko fanɗarewar daga shugaba ne ko Imami ko Khalifa to fanɗarewarsa za ta zama bala'i da hatsari a kan al'umma baki ɗaya har ma  tana iya tasiri a kan fahimtar saƙon baki ɗaya.

Alal misali idan shugaba ya kasance mai aikata saɓo ne to wane ne zai lamunce cewa ba zai yi sassauci ba ko ɗaukar matsayinsa a mafakar aikata saɓo da ɓarna ya kuma tozarta haƙƙin al'umma?

Ko kuma wane ne zai lamunce cewa ba zai bi son zuciyarsa ba wajen amfani da matsayinsa da maslaha da wata fa'ida keɓaɓɓiya?

Fiye da wannan ma wane ne zai lamunce cewa za a aiwatar da dokokin shari'ar musulunci za a aiwatar da su a aikace?

Idan har ra'ayinsa ba kuɓutacce ba ne daga kuskure to ta yaya al'umma za ta sallama ta miƙa wuya gare shi matuƙar dai ana tsammata masa kuskure?

A cikin irin wannan hali shi zai zamanto jagora ne ga wata jama'a kawai ba na al'umma baki ɗaya ba ko kuma na addini dukkaninsa ba.

A matsayin jagora shugaba ne na al'umma idan abinda ya zartar ko ya aiwatar bai dace da haƙiƙa ba to wannan zai zamanto babban bala'i ne a kan al'umma,idan shugaba zai yi ijtihadi kamar sauran malamai kuma ya yi kuskure to wannan to sakamakon kuskurensa zai zamanto ya munana ya ƙazanta matuƙa,alal misali yayin da Ɗalha da Zubair (kamar yadda wasu suke rayawa) me hakan ta haifar?Sakamakon haka shi ne kisan mutane sama da dubu 40 ko dubu 25 kamar yadda ruwayoyin tarihi suka tabbatar.

Yayin da Khalifa Usman ya yi ijtihadi ya yi kuskure ya buɗawa 'yan'uwansa da makusatansa ƙofa suka yi ta wasan kura da haƙƙoƙin al'umma da karamominta, wane sakamako yin hakan ya haifar?Yin haka ya jawo tarzoma da tashin hankali na gaba ɗaya da ya jawo fitina mai yaɗuwa da ta yi ta ci gaba na tsawon lokaci da yaƙe-yaƙe.

Yayin da Mu'awiya ya yi kuskure a nasa Ijtihadin ya tilasta ɗansa  a kan al'umma a matsayin Khalifa,mene ne ya faru? Salwantar da haƙiƙanin koyarwar addinin Musulunci rayuwar al'umma kuma da ci gabanta mai zuwa suka taɓarɓare.

Haƙiƙi saƙon musulunci saƙo ne na shugabantar duniya baki ɗaya, al'ummar Musulunci wadda ita ce al'umma mafi alheri wadda a fitar da ita ga mutane ba zai

yiwu rayuwarta ta nan gaba da makomarta su dogara a kaɗawar ijtihadi ba, da kuma canki-cankin samun daidai ko kuskure ba.Saɓanin haka ma babu makawa shugabancinta ya zamanto yana ƙarfi na kaiwa ga haƙiƙi 100% da cim ma gaskiya, musamman a wancan lokacin mai hatsarin gaske wanda musuluncin bai riga ya kammala al'umma ba kuma alamunsa da hukunce-hukuncensa ba su bayyana ba.

Wannan ita ce falsafar Isma,Imami babu makawa ya zamanto Ma'asumi domin al'umma ta natsu da maganganunsa tare da cikakkiyar amincewa da lamuncewar rayuwar al'umma ta nan gaba da kyakkyawar makomarta.

A nan ya zama wajibi mu yi tanbihi da jan hankali cewa Isma ba wai tana cewa shi Imama yana da bambanci ne na halitta da sauran 'yan Adam ta yadda aka halitta da rashin iya yin saɓo ko kuskure , a'a abin ba haka yake ba.

Abinda Isma ke nufi shi ne kaiwar Imami ga wata daraja ta ƙoli a fahimtar addini da fin ƙarfin zuciya ta yadda haka ke sanya shi yin riƙoda addini sosai da rashin fanɗarewa daga ƙa'idojinsa,a sakamakon yaƙininsa na zuciya ko kuma ƙoƙarinsa na kansa a bisa zaɓinsa da 'yancinsa.

Domin ƙara kusanto da fahimta zua ga hankali za mu ba da wannan misali kamar haka,kai ne an kawo maka zuma lafiyayyiya za ka bayan ka ɗebo ta a cokali za ka lashe sai kuda ya sauka a kanta ya riga ka, shin za ka ji cewa kana son ka shanye ta haka ne duk da cewa ƙuda ya sauka a kanta?

Tabbas ba za ka sha ba domin ƙyama ta kama ka dole ka haƙura da wannan domin ta zama ƙazanta gare ka.Amma wannan ba wai yana nufin kai ba ka sha'awar shan zuma ba ne a ɗabi'ance.Sha'awarka ta shan zuma tana nan amma ka ƙaurace mata saboda ƙyamar ƙazantar da ta auku, da zaɓinka da fahimtarka.Kana da ikon sha amma ka ƙi ka bar ta da ikonka da zaɓinka.

To haka nan Imami, ayyukan zunubi da saɓo na bayyana gaba gare don kawo wasiwasi da yaudararsa a matsayin na mutum mai sha'awa mai ɗabi'u irin na mutum amma fahimtarsa game da addini da fin ƙarfin zuciyarsa kan sanya shi ya ji ƙyama ya guje musu kamar yadda ka ji ƙyama ka ƙaurace wa zumar da ƙuda ya faɗa cikinta yayin da ka so sha da zaɓinka da ra'ayin kanka.

Imam Ali(A.S.) yana cewa:-

Alƙura'ani ya hukunta cewa Ahlul-Bayt(A.S.) ma'asumai ne a Ayar Taɗhir aya ta 33 na surar Ahzab cewa:-

"Haƙiƙa Allah kawai Yana nufin Ya tafiyar muku da datti Ya ku Ahlul-Bayt kuma Ya tsarkake ku tsarkakewa ta sosai".

Duk waɗannan da makamnatansu misalai ne na madogara da hujja game da abinda Tirmizi ya ruwaito a sahihin littafinsa,da Imam Ahmad bin Hanbal a Musnad ɗinsa da dai sauransu daga malamai shugabanni a hadisi.

Ya zo a Tafsirin Ɗabari daga babban sahabin nan Abi Sa'idul Khudri daga Ummu Salama matar Manzon Allah(S) cewa ta ce:-

"Yayin da ayar da ke cewa Allah kawai Yana nufin Ya tafiyar muku da ƙazanta ne ya ku Ahlul-Bayti sai Manzon Allah (S) ya kira Ali da Faɗima da Hasan da Husaini ya lulluɓa mayafi a kansu ya ce:Ya Allah waɗannan su ne mutane gidana Ahlul-Baytina,Ya Allah Ka tafiyar musu da datti kuma Ka tsarkake su tsarkakewa ta sosai sai Ummu Salama ta ce :Shin ni ba na daga cikinsu? Sai ya ce: ke kina kan alheri".[7]

Haka nan misalinsa a Tafsirin Ibin Kathir [8] da Durrul Mansur na Suyuɗi[9] da makamantansu na daga Tafsirai.

To tambaya na iya tasowa cewa a salon ayar yana nuni ga cewa waɗanda ake nufi su ne matan Annab (S) ta yaya waɗanda aka kawo hadisin daga gare su,Malaman Tafsiri da Hadisi suka fitar da su daga wannan aya?

Amsa:Farko dai:Mai Tafsiru Manar Malam Muhammad Abduh cewa:-

"Yana daga Ɗabi'ar Alƙura'ani ya fitar mutum daga wani hali zua wani hali na dabam sa'an nan kuma ya sake dawowa da shi zuwa wani bayanin ɗaya bayan ɗaya".

Imam Ja'afarus Sadiƙ (A.S.) yana cewa:-
"Ayar Alƙura'ani farkonta na iya zama dangane da wani abu ƙarshenta kuma ya kasance dangane da wani abin ne dabam.."

---

[7] Tarihin Ɗabari juzu'i na 9 shafi na 22
[8] Juzu'i na 3 shafi na 492
[9] Juzu'i na 5 shafi na 198.

Saboda haka a bisa wannan asasin bai dace ba a ɗauki salon aya a matsayin ƙa'ida ta gaba ɗaya.

Na biyu:A ƙaddare idan muka ce mun sallama game da salon aya to ai lamirin da ke cikin ayar "Ya tafiyar muku...Ya tsarkake ku" a larabce lamiri ne na maza ba na mata ba ne,kuma babu shakka ƙarfin nassi ya fi na salo ƙarfi.

Na uku:-Malaman Tafsiri da na hadisi da muka ambata sun yi dogaro da sahihan hadisai na Manzon Allah (S) wajen fitar da su kuma kalmar musulmai ta haɗu a kan cewa sunnar Annabi(S) ita ce fassara da bayani game da ayoyin Alƙura'ani littafin Allah.

Na huɗu:Su Imaman Ahlul-Bayt (A.S.) gaba ɗayansu sun kasance suna cewa: Mu ne waɗanda ake nufi a wannan ayar kuma babu wani da ya taɓa musa musu wannan batu.Har ila yau kuma babu wani littafi na tarihi da ya hakaito mana cewa tana da'awar wannan matsayin ba. Sai dai ma akasin haka Ummu Salama ta yi iƙrarin cewa Manzon Allah(S) ya bayyana mata a ƙarara a sarari cewa ba ta daga cikin AhlulBayt (A.S.) kamar yadda ya gabata.

Akwai hadisai da dama da Manzon Allah (S) ke yin ta'akidi game da ismar Ahlul-Bayt (A.S.) da larurar yin riƙo da su da rashin yiwuwar fanɗarewarsu daga koyarwar Aƙura'ani.

Kamar yadda Manzon Allah yake cewa:-

"Haƙiƙa ni mai barin abubuwa biyu masu nauyi ne gare ku ɗayansu ya fi ɗayan girma :Littafin Allah igiya miƙaƙƙiya daga sama zuwa ƙasa da kuma zuriyata mutanen gidana kuma su biyun ba za su taɓa rabuwa ba har su iso gare ni a Tabki."[10]

Da zarar ka karanci rayuwar Imamai(A.S.) karatu na fahimta isamarsu mai haske mai haskakawa za ta bayyana a gabanka a maganganunsu,da matsayansu da kuma ma'amalolinsu.

Ga dai Amirul Muminina Ali bin Abi Talib (A.S.) nan inda yake tabbatar da ismarsa inda yake cewa :-

[10] Mustadrak na Muhammad Hakim Naysaburi tahƙiƙi daga dokta Yusuf al-Mar'ashali3/48)

“Na rantse da Allah idan da an ba ni yankunan sammai bakwai da abinda ke ƙarƙashinsu kan in saɓi Allah game da wata tururuwa in ƙwace mata ƙwayar sha’irinta ba zan taɓa aikatawa ba,domin ita wannan duniyar taku a gurina ta fi ganye da ke bakin fara tana gingitse shi ƙasƙanci, ina Ali ina ni’ima mai ƙarewa ko jin daɗi marar dawwama,muna neman tsarin Allah daga kuncewar hankali da da mummunar zamewa. Kuma da Shi muke neman taimako.”

Haka nan a wani hadisin yana magana game da wani maatsayi nasa na isma inda yake cewa:-

“Haƙiƙa na ga Aƙilu (yaya ne gare shi) ya talauta har sai da ya roƙe ni kan in ba si alkama sa’i ɗaya kuma na ga ’ya’yansa kuma gashinsu duƙun-duƙun da duƙunduƙun ɗin launinsu ya yi baƙi ƙirin, saboda talauci, kamar an shafa musu shuni ,sun kai sun koma gare ni akai akai, ya maimaita maganganu gare ni sosai saboda haka sai na saurare shi a tsanaki har ya yi zaton zan sayar masa addinina ne in bi jan da yake yi mini in bar tafarkina;daga nan sai sanya masa ƙarfe ya yi zafi na kuma kai shi kusa da jikinsa domin ya faɗaka sai kuwa ya tsala ihu irin na mai danaf saboda zafinsa,har sai da ya kusa taɓawa ya ƙonu da shi;sai na ce masa,masu kukun mutuwa su yi maka kuka ya Aƙilu ashe za ka ji tsoron cutuwa ne ni kuma ba zan tsoron wutar Lazza ba ?”.

Shin tsakani da Allah zai yiwu mutumkamar Imam Ali (A.S.) ya kasance shi ne jagoran hukumar musulunci mayalwaciya ya takura wa kansa haka ya ƙi nuna bambanci tsakanin ɗan’uwansa da sauran musulmai a kan ɗan kilo uku na sha’iri kawai?

Sai dai kuma wannan ita ce Ismar da ya wajaba a kan jagora ya zamanto yana da ita domin ya jagoranci mutane a kan tafarkin aldalci da gaskiya da samun sa’ada.

## GAMSARWA TA ILIMI

Daga cikin muhimman nauyi da ya kamata Imam ya ɗauke shi shi ne sanya alkyabbar yaɗa saƙon addinin musulunci da bayyana shi da aiki da shi da aiwatar da shi.

Sai dai kuma shugaba ba zai iya ɗaukar wannan nauyi da ya ɗoru a kansa ba ba tare da ilimi ba, ba tare da sanin sirrin saƙon ba,ba tare da sanin hukunce-hukunce-hukncensa ba.

Wannan shi ya sa aka gindaya sharaɗin lalle Imam da zai jagoranci al'umma babu makawa ya zamanto mai ilimi dangane da dukan al'amuran shari'a,mai riskar dukkan al'amura na ɗabi'a da halitta da suka ta'allaƙa da shi da hukunce-hukuncensa na musulunci wanda hakan ne zai ba shi siffar kasancewa mafi ilim a al'umma.

Shin shi Shugaba idan ya kasance bai san hukunci ba daga hukunce-hukuncen musulunci to mene ne fa'idar samuwarsa a matsayin shugaba?Ta yaya al'umma za ta sami wancan hukuncin da shi kansa shugaban ya jahilta?

Idan har shugaba bai san al'amuran ɗabi'a da na halitta da ta'allaƙarsu da shari'a ba to ta yaya za a yi aiki da su a shari'a?

Idan har a cikin al'umma aka sami wanda ya fi shugaba ilimi to shi ya fi cancantar a bi shi kuma shi ya fi dacewa da shugabancin al'ummar.Allah Ta'ala Yana cewa:-

"Shin wanda yake shiryarwa shi ne wanda ya dacewa a bi shi ko kuwa wanda ba ya shiryarwa sai dai an shirye shi, mene ne ya same ku.Yaya kuke yin hukunci".

(Surar Yunus:35)

Wannan ta fannin hankali ke nan amma a fannin ruwaya kuwa, ya riga ya tabbata cewa Manzon Allah (S) ya yi ta'akidi ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba dangane da cancantar AhlulBayt(A.S.) da fifikonsu a kan sauran al'umma dangane da ilimi;kamar dai yadda ya faɗa a wasiyyarsa ga al'umma dangane da AhlulBayt(A.S.)

"Kada ku wuce su ku je ku halaka kuma kada ku jinkirta daga gare su ku halaka kuma kada ku koya musu domin su ne masu ilimi fiye da ku".[11]

Da kuma Magana dangane da Ali bin Abi Ɗalib (A.S.) da ya ce:-

"Ni ne birnin Ilimi Ali kuma shi ne ƙofarsa".[12]

---

[11] Saa'iƙul Muhriƙa na Shuhabuddin Ahmad bin Hajar a Babun Wasiyyar Annabi gare su.

[12] Biharul Anwar juzu'i na 28 shafi na 262.Malaman Ahlul Sunna 143 sun ruwaito wannan hadisin waɗanda Allama Amini ya kawo sunayensu da littafansu a Juzu'i na 6 shafi na 61-77 na littafin Al-Ghadir.

Dangane da tarihi da sira kuwa, ba zai yiwu ka karanta wani littafi na tarihi ko na sirar wani Imami ba face ka ci karo da sallamawar malaman zamaninsa gare a fannin ilimi tare da furtawarsu cewa shi ne mafi ilimi fiye da su, da yawa ma daga cikin manyan malamai sun yi karatu a gurinsa,Imam Ali bin Abi Talib (A.S.) dukkan sahabbai sun kasance suna yin furuci game da fifikonsa a kansu a ilimi har ma Ibin Abbas da ake wa laƙabi da tawadar al'umma ya ce:-

"Ilimina da na Sahabbai dangane da ilimin Ali ba kome ba ne face gwargwadon ɗigon ruwa ne a cikin koguna bakwai".

Khalifa Umar kuwa sau da yawa ya kasance yana zabura zuwa gurin Imam Ali da tambayoyi masu wahala domin ya san cewa amsa mai kuɓutarwa na gurinsa ;har ma ya kasance yana maimaita mashahurin batun nan nasa da yake cewa :-

"Kada Allah Ya sa in zamanto a guri matsala mai wuya babu Abul Hasan ba ya gurin".

Shi kuwa Aɗa'u Makki, dangaane da Imam Muhammad Baƙir cewa ya yi:-

"Ban taɓa ganin Malamai sun rusana a gaban wani malami ba fiye da yadda suka rusuna gaba ga Abi Ja'afar Muhammad bin Ali ba.Haƙiƙa na ga Hakam bin Utbata duk da irin girman da yake da shi a cikin mutane amma a gabansa sai zamanto kamar yaro ƙarami a gaban Malaminsa".

Abu Hanifa wanda shi ne Imamin Mazhabar Hanafiyya yana cewa :-

"Ban ga mafi sanin fiƙihu fiye da Ja'afar bin Muhammad ba"[13].

Imam Malik bin Anas shugaban mazhabar Malikiyya kuwa dangane a Imam Sadiƙ (A.S.) yana cewa:-"Na sha kaiwa da komowa zuwa gurin Ja'afar bin Muhammad na tsawon lokaci kuma koyaushe ban taɓa samun sa ba sai dai a cikin ɗaya daga cikin halaye uku :imma yana salla ko kuma yana azumi ko kuma yana karatun Alƙura'an."Ya ce : ''Idaniya ba ta gani ba,kunnuwa ba su ji ba, bai taɓa kwatantuwa a zuciya ba mafifici fiye da Ja'afar bin Muhammad As-Sadiƙ a ilimi da ibada da wara'u".[14]

---

[13] Sira A'alammun Nubala'i na Malam Shamsuddin Muhammad bin Ahmad bin Usman Az-Zahbi juzu'i na 6 shafi na 257 bugu na 9 shekara ta 1413(bugun Berut Mu'assasar Risala )

[14] Littafin Tazibut Tahzib na Shuhabuddin Ahmad bin Ali bin Hajar juzu'i na 2 shafi na 89 bugu na 1 na shekarar 1404 hijiriyya bugun Berut Darul Fikr.

Shi kuwa Abu Sultul Harawiy ya yi magana ne game da Imam Ali bin Musa Ar-Ridha (A.S.) yana cewa:-Ban ga mafi ilimi fiye da Ali bin Musar Ridha ba, Babu wani Masani da ya gan shi sai ya ba da shaida irin shaidata.Mamun ya tattaro a wani majalisi nasa wani adadi na Malaman addini,da masanan fiƙihu a shari'a da ƙwararru amma duk ya yi galaba a kansu baki ɗayansu har zuwa na ƙarshensu har babu wanda ya saura daga cikinsu har sai da ya yi furta cewa shi ne mafifici,kuma kowa ya yi iƙrari da gazawarsa."[15]

A dandalin ɗauki ba daɗi kuma za mu kawo matsayin ilimi na Ahlul-Bayti(A.S.) har darajarsu da faɗin iliminsu ya bayyana a ga kowa da kowa.

AL'AMARIN ILIMI

Wata rana Imam Ali (A.S.) ya kasance yana aiki a lambunsa,kasance yana ta kautun ƙasa da abin aikinsa,ya sanya tufafin aikinsa,yana maimaita karanta ayar da take cewa ''A YAHSABUL INSANU AN YUTRAKA SUDANN,yana maimaita karantawa yana kuka yana ci gaba da aikinsa…sai ga Khalifa Umar tare da wata tawagar jama'a daga cikin sahabbai sun shigo masa,sai ya tarye su ya yi maraba da su sa'annan ya tambaye su ko mene ne dalilin zuwansu?

Sai Khalifa ya ce: Matsala ce ta taso da babu wanda ya san warware ta daga cikin sahabbai.

Imam (A.S.) ya ce musu;alheri in sha Allahu.Me ce ce ita?

Umar:Mata ne guda biyu suka haihu tare;ɗaya ta haifi namij ɗaya kuma ta haifi mace amma kowacce daga cikinsu tana da'awar cewa ita ce mai ɗa namijin tana kore 'ya mace kuma babu wata mai shaida ko dalili a kan haka dagancikinsu .

Sai Imam (A.S.) ya ce: Wannan matsala mai sauƙi; aka kawo masa kofi ya miƙa wa ɗaya daga cikinsu domin ta tatso nono ta zuba a ciki,da ta zuba sai ya auna nauyinsa,daga nan kuma sai ya miƙa wa ɗayar ita ta tatso nata aka auna,da aka auna sai ɗaya ya rinjayi ɗaya a nauyi,bayan nan sai ba da hukuni cewa a ba da ɗa namijin ga wadda nononta ya fi nauyi marar nauyin kuma aka ba ta 'ya macen.

Sai sahabbai suka yi al'jabin wannan hukuncin nasa mata kuma suka kiɗime saboda su kan dama sun san haƙiƙanin gaskiyar al'amarin.[16]

---

[15] Biharul Anwar juzu'i na 49 shafi na 100
[16] Safinatul Bihar juzu'i na 2 shafi na 435

Ko shakka babu Imam (A.S.) ya yi aiki da ilimi wajen yanke wannan hukunci nasa,wanda shi cewa Allah Ta'ala cikin hikimarSa da Ya nufi halitta jikin namiji ya zamanta mai ƙarfi mai tsanani sai Ya nonon mahaifiya ya zamanto mai kauri mai nauyi mace kuwa da Ya nufi jikinta mai taushi mai sauƙi sai Ya sanya nonon shayar da ita siriri marar nauyi.

TSAMO HUKUNCI MAI KAYATARWA

A zamanin Imam Ridha (A.S.) wani mutumi attajiri ya yi wasiyya da cewa idan ya mutu to a 'yantar da duk wani bawansa 'ƙadim',wato daɗaɗɗe.Ilai kuwa sai ya mutu amma da aka zo aiwtar da wasiyyar sai aka gagara tantancewa ko wane bawa ne 'ƙadim' daɗaɗɗe.Saboda haka sai aka koma gurin malamai da alƙalai domin a tantance ma'anar 'ƙadim'.Sai malamai da alkalai suka sami saɓanin ra'ayi wasu suka ce duk bawan da ya yi shekara guda a gidan shi ne 'ƙadim', wasu kuwa suka ce a'a wanda ya kai shekara goma shi ne 'ƙadim' wasu suka ce a'a mai sama da goma shi ne 'ƙadim',sai dai duk wannan fatawoyi ne ba tare  da dalili ba.Daga ƙarshe sai aka kai matsalar ga Imam Ridha (A.S.) sai ya ce musu duk bawan da ya kai wata shida to shi ne 'ƙadim'.Da malamai suka ji haka sai suka tambaya she dalili,sai ya karanto musu aya daga sura ta Y.S. da ke cewa:-

"Wal ƙamara ƙaddarnahu manazila hatta ada kal urjunil ƙadim'.

Ya Allah Ya kira shi 'ƙadim' yana komawa haka ne kuma bayan wata shida.[17]

A zamanin Mutawakkil Al-Abbasi ya taɓa jinya har ya yi nazari cewa idan Allah Ya sa ya warke to zai sadaka da dukiya mai yawa sai kuwa ya warke.Bayan warkewarsa sai ya gayyato malamai domin su fayyace masa nawa ne dukiya mai yawa da ya kama ya yi sadakar da shi domin cika nazrinda ya yi. Kamar koyaushe sai malamai suka sha bamban wajen ayyana dukiya mai yawa.

Wasu suka ce ya ba da dirhami dubu, wasu suka ce bai kai haka ba,wasu suka sama da dubu,sai wani ya ba shi shawara cewa ya tambayi Imam Ali Al-Hadiy (A.S.).A lokacin kuwa dama Imam (A.S.)yana tsare a kurkukun Mutawakkil ɗin saboda haka sai ya sa aka tambaye shi.Sai Imam (A.S.) ya amsa da cewa ya yi sadaka da dirhami tamanin.

---

[17] Tafsiru Majma'ul Bayan na Malam Ɗabrisi juzu'i na 8 shafi na 32 bugu na1 shekara ta1415hijiriyya bugun Berut Mu'assatul A'alamiy lil Mutbu'at.

Sai Malamai suka bayyana rashin yardarsu kuma suka nemi dalili daga Imam(A.S.) sai ya amsa musu da ayar da Allah ke cewa:-

“Laƙad nasara kumullahu fi mawaɗina kathiratin”.To mun ƙididdige gurare da yawa ɗin nan mun iske su tamnin ne.”[18]

RIGE-RIGE DA ILIMIN KIMIYYA

A sakamakon sani asirran al’amura da Imamai (A.S.) suke da shi ya kasance abu ne mai yiwuwa gare su yin ishara ga haƙiƙanin al’amura na ɗabi’a da na halitta, idan ba domin gajiyawar al’umma da jama’ar zamaninsu ba wajen iya fahimta da gane haƙiƙanin al’amuran ba a wancan zamanin amma kuma duk da haka Imamai(A.S.) sun bayyana wasu al’amura na haƙiƙanin ilimin kimiyya tun ma kafin zamani bincike da ƙage-ƙage.

A lokacin da Imam Ali bin Abi T lib (A.S.) yake tafiya zuwa yaƙin Naharawan sai ya ga wani kwazazzabo ruwa na kwararowa daga gare shi sai ya ce :-

“Idan da na so da zan iya fitar da haske wanda dukkan duniya za ta iya haskakawa da shi”.

Wannan batu ne da ya gabata ya wuce sannu-sannu da shuɗewar zamani amma rayuwar teku da koguna a yau su ne maɓuɓɓugar samar da hasken wutar lantarki alhali Imam (A.S.) tun shekara dubu da ɗari takwas ya yi ishara ga yiyuwar samar da haske daga ruwa.

Wata rana Imam Ali(A.S.) ya kasance yana tafiya daga Hijaz zuwa Iraƙi sai ya yada zango a wani guri mai yashi da tsakuwoyi a cikin hamada inda ya fara jujjuya yashin yana magana da sahabbansa yana cewa idan da na so da sai in fito muku da man fetur daga cikin wannan ƙasar! Sai suka ce:mene ne man fetur? Sai ya ce wani abu ne mai kama da kama da mai na girki”.[19]

Abu ne sananne cewa baban ilimin ‘Kemestiri’ shi ne Jabir bin Hayyan Kufiy aljimirin Imam Ja’afarus Sadiƙ(A.S.) wanda fara kowane babi da ya yi bayani a littafin kemestirin,kamar yadda yake a yanzu haka a gidan ajiyar abubuwan tarihi

---

[18] Tafsiru Majma’ul Bayan juzu’i na 5 shafi na 32.

[19] Mujallar Huda ta Kuwait adadin watan Ramadhana shekarar 1976 da naƙalto dagaa Mujallar Irfan ta ƙasar Lebanon.

a London,ya fara kowane babin littafin da cewa:- “Shugabana Ja’afar bin Muhammad Sadiƙ ya gaya mini.[20]

Imam Sadiƙ (A.S.) kuma shi ne wanda ya riga kowa wajen bayani game da zazzagawar jini a jikin mutum da kuma cewa tsirrai su ma suna da rai, da dai sauran al’amura makamantansu masu zurfi[21].

Imam Ridha (A.S.) kuwa ya yi ishara game da maganaɗisu da ke cikin ƙasa yayin da aka yi masa tambaya dangane da faɗin Allah Ta’ala da ke cewa: “Wassama’i zatil hubuk”,ya ce, “Mahbukatun ilal ardhi wash shabaki bayna asabi’ahu...”[22]

Amma dangane da ko ta yaya Imamai (A.S.) suka kai ga wannan darajar kuwa ta ilimi da sanin hakikanin al’amura da yadda suka mallaki wannan wadatuwa ta ilimi mai tarin yawa?Wannan yana iya yiwuwa ne ta musabbabai daban-dabam kamar haka:-

1.Bambantar su da ƙarfin ƙwaƙwalwa da hadda.

2.Tarbiyya da ilmintarwa,domin kowane Imami ya kasance yana samun karantarwa da ilmantarwa daga Mahaifinsa dangane da ilimi da fahimta game da rayuwa a jejjere har ya kai ga Imamin da ya koya kuma ya tarbiyyantu a gurin Manzon Allah (S)

3.Ilhami daga Allah Ta’ala,ta hanyar gaibi Allah ke cusa ilimi da fahimtar da Imami ke a ruhinsa da tunaninsa.

Ilhami hanya ce da Allah ke amfani da ita ba wai kawai ga Annabawa ba a’a har ma ga har ma ga waliyyai da salihan bayi waɗanda hikimar Allah da iradarSa ta sanya yin haka.Alƙura’ani mai girma ya ba da labarin sadarwar saƙon samaniya daga mahaifiyar Annabi Musa (A.S.) cewa:-

“Kuma Muka yi wahayi ga mahaifiyar Annabi Musa cewa ki shayar da shi amma idan har kika ji tsoro to ki jefa shi kada ki toro kuma kada ki yi baƙin ciki Mu lalle za Mu dawo zuwa gare ki kuma za Mu sanya shi daga cikin Manzanni”.

(Surar Kasas aya ta 7) .

---

[20] Littafin Imam Sadiƙ (A.S.) kama arafahu ulama’ul Gharb.

[21] Littafin Tawhidul Mufaddhal

[22] Tafsirul Majma’ul Bayan juzu’i na 9 shafi na 254

Dangane da ƙisar Maryamu mahaifiyar Annaabi Isa kuwa (A.S.)yana cewa:-

"Sai ta riƙi gurin shamaki da ke ba gurinsu ba ne sai Muka aika mata RuhinMu gareta ya bayyana a gare ta da siffar mutum daidai.Ta ce masa ni ina neman tsarin Mai Rahama daga gare ka idanka kasance mai kiyayewa ne .Sai ya ce :Ni kawai Manzon Ubangijnki ne domin in ba miki yaro tsarkakakke". (Surar Maryam aya ta 17-19)

Saboda muhimmancin aikin da Imami ke gudanarwa sai Allah Ta'ala Ya ƙarfafa shi da dukkan wani abu da maslahar addini ke bukata na ilimi da fahimta.

Wannan shi ne abinda wasu zahirin al'amura na gaibi ke fassara mana dangane da rayuwar Imamai (A.S.),kamar irin yadda suke fito da wasu al'mura na gaibi da ba da labarinsu dangane da abubuwan da za su auku nan gaba,da zurfin iliminsu a ƙarancin shekaru,kamar Imam Jawad (A.S.) da ya dauki nauyin Imamanci tun daga shekarun yarinta,kuma ya iya ya yi rata a kan manyan malaman zamaninsa a ilimi.

ƊAUKAKAR KOLI TA KOWANE ƁANGARE

A ɓangaren farko mun yi bayani dangane da larurar Imamai su zamanto a aikace masu aiwatar da koyarwar 'yan Adamtaka na ƙoli domin su zamanto ababan koyi ga mutane a kan su waɗannan sifofin masu kyawun a aikace har ila yau kuma su zamanto hujja a kan jama'a da kuma kasancewa waɗanda suka sanya alkyabbar falala da kawo gyara.

Abin nufi shi ne Imamai su zamanto suna kan darajar ƙoli wajen aiwatarawa da siffantuwa da siffofi maɗaukaka a wata fassara kuma mu ce su zamanto su ne maɗaukaka na ƙoli a dukkan ɓangarori na falala da ƙa'idoji da alherai a aikace.

Idan kuwa ba haka idan har Imami ya zamanto yana da wata tawaya a wata halayya ta ƙwarai to wannan na nufin an samu giɓi ke nan a jagorancin al'umma wanda haka na iya buɗe ƙofa ga guguwar koma-baya ko kuma fanɗarewa da kauce hanya.

Alal misali idan Imami ya kasance yana da dukkan kyawawan ɗabi'u ko sifofi amma kuma ya rasa kyakkyawar sifar jarumtaka da zabura kan gaba,wannan zai haifar da karayar zuciya da tsoro a al'umma wajen yin fito-na-fito da abokan gaba;wannan zai yi tasiri mummuna a kan kowane ɓangare na al'mma wanda zai

kai ga mummunar koma-baya ga al’umma da karyewa a fagagen fama da bakin dagar yaƙi.

Idan kuma Imam ya kasance yana da dukkan kyawawan siffofi amma sai ya zamanto yana da tawayar siffar adalci,to wannan zai sabbaba naƙasa a sikelin auna aiki da gaskiya da adalci tsakanin shugaba da jama’ar da yake shugabanta,wannan kuwa zai iya haifar da barkewar rigingimu da tarzoma tashin tashina a  al’umma.

To domin a yi riga-kafin aukuwar wannan ɓarakar babu makawa Imami ya zamanto yanan da dukkan kyawawan sifofi ta kowane fanni ba ma wannan kawai ba ya wajaba ya zamanto shi ne mafi ɗaukaka ta ƙoli a dukkan kyawawan sifofi da ɗabi’un ƙwarai a dukkan ɓangarori domin ya zamanto abin koyi ga kowa da kowa a l’umma.

Dangane da Isma kuwa mun ga yadda su Imamai suka bambanta da cikkakken riƙo da haƙiƙanin koyawar addini ba tare da zurfafawa wajen aiwatar da koyarwar addini a cikin girman al’amari ko mafi ƙarancinsa.

Kamar kuma yadda ya bayyana a gare mu a sarari yadda suka ɗara kowa a ɓangaren ilimi da sanin haƙiƙanin al’amura.

A wannan ɓangare muna so mu kawo bayani don tabbatar da yadda suka ɗara kowa a sauran fannoni, wasu daga misalai su ne kamar haka:-

JARUMTAKA DA TSAYUWA DAIDAI

Jarumtaka da tsayuwa daidai a dukkanin fagagen fafatawa a rayuwa da gogayya da ita,ba wai a fagen yaƙi ba ne kawai sai dai fagen yaƙi kawai shi ne mafi bayyanar da jarumtakar mutum da tsayuwar daidai ɗinsa,jarumtaka ta fagen yaƙi kuwa ba ta samuwa sai daga wanda yake da ruhi mai tsayuwar daga da zuciya mai ƙarfi,haka nan wani reshe ne na ƙarfin hali.

Al’ummar Musulunci tunda yake tana fuskantar barazana ta kowane ɓangaren jahiliyya da zalunci da fandarewa saboda haka tana da mafi tsananin bukatar halin jarumtaka da tsayuwar daka.

Amma wannan al’umma daga ina za ta samo wannan jarumtakar da tsayuwar dakan da kuma zaburarwa?

Imaman AhlulBayt tsarkakakku(A.S.)tunda yake su ne jagororin al’umma sun kasance suna siffantuwa da jarumtaka ta ƙoli da tsayuwar daka mafi ƙarfi.Sadaukarwaru da ruhinansu sun rubuta wa tarihi irin gagara badau ɗin jarumtakarsu gwarzantakar fafatawarsu.

1.A yaƙin Khandaƙ,ranar da jam’iyyu da ƙabilu suka yi gangami suka kewaye garin Madina,musulmai sun yi aiki tuƙuru na tonon ramin lambatu mai faɗi mai zurfi domin kewaye garin Madina da shi sboda hana maƙiya tsallakawa zuwa cikin grin,sai dai kuma wasu gwarzaye daga cikin Kuraishawa sai da suka gane wani guri marar faɗi sosai inda suka tsallaka cikin garin da dawakansu,wannan garnaƙaƙin ƙato mai suna Amru bin Abdi Wuddi shi ke musu jagora,shin sanannen gwarzo,da suka iso kusa da rundunar Musulmai sai ya yi kirari ya yi ƙalubale ga Musulmai ko akwai wanda zai fito ya iya karawa da shi.

Sai Manzon Allah (S) ya dubi sahabbansa ya ce musu: “Wane ne zai iyar mini wannan?

Babu wanda ya amsa sai Ali(A.S.) ya amsa ya ce: “Ni ji da shi ya Annabin Allah”!

Sai Manzo(S) ya ce masa: “Zauna ;Amru ne fa”!

Sai Amru ya ƙara maimaitawa a karo na biyu tare da yin izgili,babu namiji ne?Ina Aljannar taku da kuke da’awar cewa wanda aka kashe shi daga cikinku zai shige ta?

Sai Ali (A.S.) ya zabura da shauƙi yana cewa:-“Ni zan ji da shi ya Manzon Allah.Sai Manzon Allah (S) ya sake umartar sa da ya zauna domin y aba da dama cikakkiya ga amsa ƙalubalen.Amma sai Amru ya ƙara zanƙewa yana barazana yana waƙe yana cewa:-

‘’Haƙiƙa na ƙosa ga kirari

Taron ko da mai amsa kirari ?

Na tsaya mai tsoro fa ya karaya

Matsayin gwarzo mai ba da kariya,

Haka nan nake ban canja ba ni

Mai kai hari ga masu .....

A nan ne sai Ali (A.S.) ya ji cewa ƙalubalen fa ya kai darajar intaha haka kishin mai da martaninsa kuma ya zo ƙoli don haka tashi ya isa gurin Manzo(S) ya roƙi izinin ya je ya kara da shi.

A wannan karon sai Manzon(S) ya ba shi izini ya kuma tashi yana masa rakiya yana duban sa duban ƙauna da tausayawa yana cewa:-

"Imani baki ɗayansa ya fita zuwa ga kafirci dukkaninsa."

Yayin da Imam Ali (A.S.) ya isa kusa da shi sai Amru ya dube da mamaki yana cewa:-"Wanene kai?"

Ya amsa masa da cewa "Ali bin Abi Talib.

Sai Amru ya ce a'a ai Babanka da abokina ne koma abinka ba na so in kashe ka.

Imam Ali (A.S.) ya ce masa: Amma ni kuma ina so in kashe ka.

Amru ya ce:Ya ɗan ɗan'uwana ni ina ƙin in kashe mutum ɗan daraja kamar ka koma abinka ɗan baffanka bai yi imani da wannan mashin nawa ba tun da ya turo ka gare ni in tsage ka in bar ka shanyayye tsakanin sama da ƙasa ba ka da rai kuma ba ka mutu ba.

Sai Imam Ali (A.S.) ya ce masa : "Haƙiƙa ɗan baffana ya sani cewa idan ka kashe ni to zan shiga Aljanna kai kuma za ka shiga wuta,idan kuma ni na kashe ka to kana wuta ni kuma ina Aljanna".

Sai Amru ya ce : "Duk yadda ta kaya biyun kai da su ya Ali? Wannan kuwa ai kasafi ne nakasasshe".

Sai Imam Ali(A.S.)ya ce masa:Kuraysh na da'awar cewa ba a yi maka tayin abubuwa uku face ka amsa ɗaya daga cikinsu.

Amru ya ce:Haka yake.

Imam ya ce masa:To ina kira gare ka yi kalmar shahada ka ce;Babu abin bautawa sai Allah kuma Muhammadu Manzon Allah ne.

Amru ya ce: A'a ka bar wannan batun.

Imam(A.S.) ya ce masa:To ka koma Makka kai da waɗanda suka zo tare da kai idan Muhammadu gaskiya yake yi to idanku na nesa da shi,idan kuma ƙarya yake yi to ƙabilun labarawa sun iyar muku al'amarinsa.

Amru ya ce:Ai matan Kurayshawa za su yi ta yin magana ta su ce yaro ƙarami ya yaudare ni,za su ta waƙe game da ni suna cewa na ji tsoro na ja baya a yaƙi ko na bar mutanen da suka naɗa ni in shugabance su.

Sai Imam(A.S.) ya ce masa:To ina kira gare ka da ka sauko mu yi yaƙi a ƙasa.

Amru ya yi al'jabi:Ban taɓa tsammani wani daga cikin Larabawa zai taɓa gwada yin haka da ni ba.Daga nan sai ya sauko daga dokinsa ya yi wa Ali shigar sauri ya kai masa sara a ka,bai same shi ba,daga shi kuma sai ya makaifa ya mai da martani ya same shi ya yi masa mummunan sara a wuya ya haɗa da ƙafofinsa biyu sai ga Amru shirim ya faɗi a ƙasa,yaƙi ya ƙare Musulmai sun ci nasara.

A taƙaice a duk wani yaƙi da aka je da Musulmai matsayin Imam Ali na gwarzantaka ke yanke hukuncin yaƙin ya kai musulmai ga cin nasara.

TSAYUWAR DAKAN IMAM HUSAIN

Dukkan sahabbansa sun sadaukar da rayukansu,sun ba da rayukansu fansa ga musulunci jikkunansu na kwakkwance nan a kan ƙasa,kuma an kashe dukkan 'ya'yansa maza har ma da jariri mai shan mama an karkashe su da takkuban zalunci da ƙetare haddi...Sai ya saura shi kaɗai a fagen fama,yana fuskantar wannan babbar rundunar mayaƙan masu manyan da yawan adadi amma ya kasance ma'abucin tsayuwar daka, ya tsaya daidai,tsayuwa ƙyam a kan digadigansa ruhinsa kuma yana nan daram haka nan ya yi ta gwabza yaƙi ya rera take yana cewa:-

Ni ne Husaini ɗan Ali

Na tattaro ba na yin gantali

Zan kare iyalan abbana abiy

In zarce a kan addinin Annabi.

Humaidu bin Muslim,wanda ya halarci bakin daga ya kuma ga fafatawar da idonsa, yana cewa:-

"Wallahi ban ga wanda aka gallaba koda sau ɗaya ba, an riga an kashe 'ya'yansa da mutanen gidansa da sahabbansa amma ya ɗaure makami ko ya koma gefe ko kuma ya guje ya yi gaba, wallahi ban taɓa gani kafin shi ko bayan shi kwatankwacinsa ba, mazaje sun kasance suna zaburo masa shi kuma ya zabura

kansu da takobinsa,sai su dare su ba shi guri hagun da dama,darewa irin ta awaki idan kura ta kai musu farmaki,ya kasance yana kai musu hari duk su tarwatse tamkar fara wanda take barkate a ko'ina da ina sa'annan ya koma gurinsa yana yawaita faɗin "la haula wa la ƙuwwata illa billah"

FAFATAWAR IMAMAI

Imamai daga 'ya'yan Imam Husain(A.S.) sun ci gaba da jagorancin bijirewa da ƙalubalantar shugabancin zalunci,da yanayin fasadi da lalacewa;sai dai kuma halin yanayin ya sanya sun canja salon yin aiki ta wata hanya ayyananniya ta daban,ta koyarwa da wayar da kan al'umma game da sahihiyar koyarwar saƙon Musulunci,da ba shi kariya da katange ainihin ƙa'idojin addini da kuma al'umma.

Wannan shi ne dalilin da ya sa za a iske a zamunnan Imamai a koyaushe cike suka da juyin juya hali.

A zamanin Imam Zainul Abidin (A.S.) an sami "Yunƙurin Tawwabin" da kuma juyin juya halin Mukhtar Aththaƙafiy.

A zamanin Imam Baƙir kuma ɗan'uwansa Zaid bin Ali shi ya yi yunƙuri.

Bayan kashe shi kuma sai ɗansa Yahya bin Zaid shi ma ya yunƙura.

A zamanin Imam Sadiƙ (A.S.) an yi yunƙurin Abdullahi bin Mu'awiya bin Abdulmalik bin Ja'afar bin Abi Ɗalib,bayansa kuma sai yunƙurin Muhammad bin Abdullahi Zin Nafsiz Zakiyya wanda yake daga jikokin Imam Hasan bin Ali bin Abi Ɗalib.Haka nan a daidai wannan lokacin aka sami yunƙurin ɗan'uwansa Ibrahim bin Abdillahi.

A zamanin Imam Kadhimkuma aka sami yunƙurin Husain bin Ali Shahid Fakh. Da kuma yunƙurin Yahya da Idris bin Abdullah.

A zamanin Imam Ridha kuma an sami yunƙurin juyin Muhammadu bin Ibrahim da Abi Saraya sai kuma yunƙurin Muhammad Dibaji bin Ja'afarus Sadiƙ,sai yunƙurin Ali bin Muhammad bin Ja'afarus Sadiƙ,sai kuma yunƙurin Ibrahim bin Imam Kadhim.

A zamanin Imam Jawad ne kuma aka sami yunƙurin Abdurrahman bin Ahmad daga cikin 'ya'yan Imam Jawad(A.S.) da kuma yunƙurin Muhammad bin Kasim daga jikokin Imam Ali(A.S.).

Haka nan dai a zamunna daban-dabam na Imamai aka yi ta samun tashin-tashina da yunƙuri iri daban-dabam da yin artabu da zalunci da fasadi.

Duk da cewa tarihi bai kawo mana alaƙar Imamai (A.S.) da waɗannan yunƙurorin da kuma jagororinsu ba sai dai kuma a taƙaicen taƙaitawa ya kawo mana yabawar Imamai ga shugabannin waɗann yunƙurorin,da irin takaicin da suka ji game da makomarsu ko karyewarsu, a'a ba ma kawai ba har ma da gudummawarsu gare su ta hanyar tattalin arziki ko ma ƙyale 'ya'yansu shiga sahun yunƙurin.

A korewa da matsawar da shugabanni azzalumai suka kasance suna yi wa Imamai da kuma ɗaure su a gidajen kurkuku akwai dalilan jin cewa su Imaman sun zamanto ƙarfan ƙafa ne ga azzaluman na zamaninsu; idan kuma da ba haka ba ne to me ya haɗa shugaba da Imami da ya duƙufa a zuhudu da ibada kawai?

Bugu da ƙari kuma yawancin  masu yunƙurin sun kasance daga 'ya'yan Imaman ne ko almajiransu ko mabiyansu.

KYAWUN ƊABI'UN KWARAI

A ta ɓangaren ayyukan zamantakewa kuwa da kawo gyara na gaba ɗaya ɗabi'un ƙwarai na da darajar ƙoli a muhimmanci.Su ne ke ayyana maslaha da jagora da farkar da mutane da jan hankulansu da canza zukatansu tare da sanya su amsa kiran su  zuwa ga wannan yunƙuri tare kuma da raunana matsayin maƙiya da tilas ta su su canja matsayi game da ma'abuta yunƙurin.

Imamai tsarkakakku(A.S.) kuwa a matsayinsu na jagorori a zamantakewa masu shiryar da mutanen al'umma da gyara su saboda haka babu makawa su zamanto masu kyawawan ɗabi'u na darajar ƙoli ta yadda za su iya aikata wajibinsu da isar da saƙonsu.

Mutum na iya cika da mamaki sosai idan ya karanta salon rayuwar Imamai(A.S.)a zamantakewa da kyautata ɗabi'unsu a ma'amalarsu da mutane mabambanta a matsayi da ɗabaƙoƙi,ta irin kyautawa gare su, da tausaya musu da taimaka musu,da irin mutuntawarsu ga kowa da kowa da kame kansu daga ɓata wa wani,maƙiyi ko masoyi.

A nan za mu kawo wasu shaidu daga ɗabi'un ƙwarai daga Imamai (A.S.):-

1.A lokacin da Imam Ali(A.S.) ya kasance shugaban babbar daular Musulunci sai wani mutum tare da ɗansa suka kai masa ziyara .Sai Imam(A.S.) ya karɓi

baƙuncinsu ya sa aka sanya shinfiɗar abinci kuma aka kawo abinci aka ci,da aka gama cin abinci sai mai hidima ya zo da butar ruwa da kyalle don wanke hannu sai aka ga Imam (A.S.) ya tashi ya karɓi butar zai zubawa baƙon nasa ruwa domin ya wanke hannu.

Sai mamaki ya kama wannan baƙon ta yaya zan yarda  Imamin al'umma shugaban hukuma?

Sai mutumin ya ƙi yarda da haka yana cewa : "Ya Imam kada Allah Ya nuna mini kana zuba mini ruwan wanke hannu.

Amma sai Imam(A.S.) ya matsa sai ya zuba masa,cikin girmamawa da ƙanƙan da kai.Da ya gama zuba wa baƙon sai kuma ya miƙa butar ga ɗansa Muhammad bin Hanafiyya daomin ya zuba ɗan shi mutumin yana cewa ya ɗana idan da wannan ɗan shi kaɗai ya zo mini to da nine zan zuba masa ruwan wanke hannun amma Allah ba Ya son a daidaita tsakanin ɗa da uba idan sun haɗu a guri ɗaya saboda haka tunda uba ya zuba wa ɗa to shi kuma ɗa sai ya zuba wa ɗa.[23]

2.Wata rana idi da sassafe sai wata baiwar Imam Husain (A.S.) ta yi masa kyautar fure don barka da ranar idi.

Sai Imam (A.S.) ya karɓa cikin murna da farin ciki yana godiya ya ce mata: Na 'yanta ki saboda Allah.

Waɗanda suke tare da shi duk sai suka yi al'ajabi suka ce masa ba kome ta yi maka ba illa dai ta ba ka ɗan reshen fure ne kawai wadda ba a bakin kome take ba.

Sai ya ce musu:- "Haka Allah Ya ladabtar da mu, Allah Yana cewa:-

"Idan aka gaishe ku to ku amsa gaisuwa da wadda ta fi ta ko kuma ku mayar da ita".Ni ban ga amsa gaisuwar wannan baiwar fiye da 'yanta ta ba saboda haka na 'yanta ta saboda Allah.

2. A zamanin Mamun Al-Abbasiy  shugaban mulkin Banu Abbas Imam Ali Ridha bin Musar Ridha (A.S.) ya kasance shi ne a matsayin mai jiran gado kuma an kasance an sanya masa shinfiɗar cin abinci mayalciya shi kuwa sai ya kirawo masu hidimarsa baki ɗaya ya zauna ya ci tare da su gaba ɗaya.

---

[23] Biharul Anwar juzu'i na 41 shafi na 56

Wata rana sai wani daga cikin muƙarraban hukuma ya halarci cin abinci da shi amma da ya ga talakawa da masu hidima tare da shi sai ya bukaci Imam Ridha (A.S.) cewa ko za a ware musu nasu gurin cin abincin dabam;sai Imam (A.S.),sai Imam (A.S.)ya ce masa:-
"Haƙiƙa Ubangiji ɗaya ne, uwa ma ɗaya ce,uba ma ɗaya ne,sakamako kuwa za a yi ne gwargwadon ayyuka''.[24]
4.Wata rana Mutawakkil Abbasi ya ba da umarni ga wani badakarensa mai suna Sa'idul Hajib cewa ya je gidan Imam Ali Al-Hadi (A.S.) ya yi titsiye ya bincike gidan ya zo da duk abinda ya samu a gidan kuma ya kamo Imam ɗin ya zo da shi.Saboda haka sai wannan badakaren ya isa gidan cikindare ya sanya tsani ya hau ta katangar bayan gida amma ko da ya tsallaka ya shiga ciki sai ya kasa ganin kome saboda duhu ya kuma ruɗe, sai kawai ya ji Imam ɗin na ce masa; tsaya nan inda kake har in zo maka da fitila.
Badakaren ya ce: "Sai kuwa ga shi Imam ya kawo mini fitila na hashaska na bincike gidan".[25]

IBADAR KOLI

Ita ibada ba wai sarrafa jiki kamar yadda kawai yadda aka iske iyaye da kakanu suna yi ba ne; tsayuwa, zama da dudduƙawa kawai.

Haka nan kuma ba wasu kalmomi ba ne masu  masu rikirtawa da a yi ta maimaita su ba tare da fahimta ko sanin ma'anarsu ba.

Haka nan ba ware kai ne mutum ya guje wa matsalolin rayuwa ba ya yi ta zuhudu yana guje wa duniya.

Haƙiƙanin ibada ita ce natsuwa ,tuntuntuni da tarbiyya kai da ruhi wadda take kai mutum ga tsarkaka da soyayya da kyakkyawar niyya tare da tsaftace masa datti irin na hasada da ƙufe da fanɗarewa.

Ibada ƙanƙan da kai ne na ruhi wanda ke bayyana a jiki wadda a sakamakonta mutum ke ƙimarsa a wannan duniyar mai girma da wajibinsa a gurin Allah Mahaliccin kome kuma mai gudanar da kome a halittu.

Ibada samun ilhami ne na ɗaukakar ruhi da ƙa'idar gaskiya da tarbiyyantar da rai.

---
[24] Biharul Anwar juzu'i na 50 shafi na 101
[25] Biharul Anwar juzu'i na 50 shafi na 199

Wannan ita ce yadda Imamai suka kasance sun fahimci ibada kuma da wannan fahimtar suka kasance suna aiwatar da ita har suka zamanto misali abin koyi a ƙan-ƙan-da-kai; a nan kuma za mu kawo wasu misalai daga irin ibadar Imamai(A.S.)

1. Abu Darda yana ba mu labarin ibada ta ban al'ajabi da ya gani idonsa a gurin Imam Ali (A.S.) ya ce:-"Wata rana na ga Ali bin Abi Talib(A.S.) a tsakanin bishiyoyi ya ware kansa nesa daga mabiyai da sahabbansa, haka ni ma ya yi nesa bana gane ko shi wanene shi,sai na ji sautin baƙin ciki da takaici yana cewa:-

"Ya Ubangijina sau nawa ne abu mai halakarwa na yi juriyarsa a maimakon narkon azabarka?Laifi nawa ne Ka yi karimci ba Ka fallasa shi ba karamcinKa? Ya Ubangijina idan har aikata saɓona ya tsawaita a shekarun rayuwata,kuma zunubina ya girmama a cikin littafina to ba ni da sanya tsammanin wani abu sai dai gafararKa kawai kuma bana taɓa sa rai a kome sai samun yardarKa kawai".

Koda sauti ya yi galaba a kan ji  na bi diddigi na ƙara natsawa sai na gane Ali bin Abi Talib ne saboda haka sai na ɓuya masa na dena motsi har ya yi raka'o'i a cikin duhun dare daga ya kama addu'a yana kuka tare aibata kai yana cewa:-

"Ya Ubangijina idan na tuna afuwarKa sai kurakuraina su ƙaranta a gare ni idan kuma na tuna da girman kamun azabarKa sai bala'ina ya girmama a gare ni..aah.

Idan na karanta littafin munanan ayyukana waɗanda na riga na mance su alhali Kai Ka kiyaye Kana sane da su; tamkar Kana umarni da cewa "ku kama shi, ya kaitona na kamo ni da za a yi kamarwa da dangi ba za su iya taimakawa ba gare ni,kaitona ga kamu wanda ƙabilata ba za iya taimka kome ba..wayyo ni ga zafin wuta mai ɓararraka ƙoda da hanta mai zagwanye jiki baki ɗaya,wayyo ni daga ƙunan wuta mai kwaye fatar makwarkwaɗa wayyoni game da falfalin wutar lazza".Daga sai ya fashe da gunjin kuka.

To ka ga yadda Imami ke tarbiyyantar  da kansa a ta hanyar ibada?Yadda yake kushe kansa da zargin zuciyarsa?Amma kada ka manta wannan fa shi ne jarumin nan gwarzon yaƙi ƙi-gudu sa-gudu a fagen fama.

2. Gumurzun yaƙi yana ta ci gaba tsakanin adadin muminai 'yan ƙalilan ma'abuta tsayuwar daka waɗanda su ne sahabban Imam Husain (A.S.) da

kuma gungun babbar rundunar mayaƙa masu yawa maha'inta mayaƙan Yazid,ana tsaka da fafatawa gawarwaki na ta faffaɗowa daga kan dawakai,hannaye kuma suna ta tsittsinkewa a sakamakon yayyankewar takubba,jinni kuma yana ta kwarara yana rina ƙasar Karbala, garjin rana kuma ya kai matuƙa daga falfalinta daga sama amma a cikin wannan lokacin na ƙuntata da damuwa sai wani daga cikin sahabban Imam Husain (A.S.) mai suna Abu Samama Assaydawiy ya koma gurin Imam Husain(A.S.) yana cewa:-
"Ya Aba Abdillah raina ya zama fansa gare ka waɗannan maƙiyan fa sun ƙara kusantowa zuwa gare ka amma wallahi ba za a kashe ka ba har sai

an kashe ni tare da kai har sai na yi wannan sallar tare da kai.

Daga sai Iman Husain (A.S.) ya ɗaga ido ya dubi sama ya ce : "Ka ambaci salla to Allah Ya sanya ka a cikin masallata masu zikiri,haka ne lalle yanzu ne farkon lokacinta sa'an nan sai ya ce: ku roƙe da su dakata mana mu yi salla, sai suka roƙe su amma kuma jama'ar Umar bin Sa'ad sai suka yi izgili da roƙon da aka yi musu.Imam(A.S.) da jama'arsa suka yi ta amfani da hanyoyi daban-dabam don ganin sun yi salla har dai daga baya suka amince suka tsagaita wuta don haka Imam Husain (A.S.) ya wuce gaba limanci wasu daga cikin sahabbansa sauran kuma suna ba da kariya ga waɗanda suke salla.

Ana cikin yin salla sai wani ya cillo kifiya ta nufo Imam Husain(A.S.) sai wani daga Imam Husain(A.S.) da ake kira Sa'id bin Abdillahil Hanafiy ya sa ƙirjinsa ya tare ta domin kada ta kai ga Imam Husain (A.S.) sai dai kuma kifiyar ba ɗaya ba ce ba biyu ba,har kifiyoyi goma sha biyu ne suka biyo baya duk kuwa suka kakkafu a ƙirjin wannan jan namiji nan ya faɗi ya yi shahada Imam (A.S.) kuma ya idar da salla cikin gaggawa.

Haka Imam Husain (A.S.) ya ƙetara da sallarsa a cikin hari a bakin daga; haka ya koya mana muhimmancin ibada hatta a cikin yanayi mai tsanani.

3.Imam Ali bin Husain(A.S.) a tarihi sananne ne a ibada da addu'a har ma ya shahara da laƙabin Zainul Abdin..to amma yaya ibadar tasa ta kasance? Me yana nufi da addu'arsa?

Biyo ni ka kranta wannan yanki daga addu'arsa mai ratsa jiki mai tasiri ka lura da irin salon tarbiyyar da yake bi ta hanyar addu'a domin cusa wa rai da zukata ƙa'ida da falala da ƙarfafa su da zurfafa su a cikin zukata.Yana cewa:-

"Godiya ta tabbata ga Allah Wanda nake kiranSa kuma Ya amsa mini koda kuwa ni ina yin jinkiri yayin da Shi Ya kiraye ni.Godiya ta tabbata ga Allah Wanda nake roƙon Sa kuma Ya ba ni koda kuwa ni mai yin rowa ne yayin da Ya yi umarni in ba da bashi saboda Shi,godiya ta tabbata gare Shi Wanda nake yin kira gare Shi duk lokacin da na so, in kaɗaita da Shi don wata bukatata yadda na so da sirrina ba tare da wani kamun ƙafa ba kuma Ya amsa mini bukatata.

Godiya ta tabbata ga Wanda ba na sa tsammanin wan ba Shi ba,koda kuwa na sa tsammani ga wani ba shi ɗin ba to da ya saɓa wa tsammanin nawa,godiya ta tabbata ga Allah Wanda Ya dogarar da gare Shi Ya mutunta ni bai dogarar da ni ga waninSa ba ballantana ya walaƙanta ni, godiya ta tabbata ga Allah Wanda yake soyayy gare ni alhali Ya wadatu ga bari na, godiya ta tabbata ga Allah Wanda Yake haƙuri da ni kamar dai ba ni da wani zunubi,saboda haka Ubangijina Shi mafificin yiwa godiya a gurina kuma Shi ne mafi haƙƙin samun godiyata".[26]

"Ya Allah Ka yi da tsira ga Muhammadu da zuriyarsa kada Ka ɗaukaka ni zuwa ga wata daraja a cikin mutane har sai Ka saukar da ni ƙasa gwargwadonta a cikin zuciyata, Kada Ka samar mini wani fifiko na zahiri har sai Ka farar da ƙasƙantuwa ta baɗini kwatankwacinsa.

Ya Ka yi daɗin tsira ga Muhammadu da zuriyarsa,Ka ba ni shiriya ta ƙwarai wadda ba zan taɓa neman musayenta ba,da hanyar gaskiya wadda ba zan taɓa kauce mata ba har abada,da niyyar shiriya wadda ba na taɓa shakka a cikinta har abada.

Ya Allah Ka yi daɗin tsira ga Annabi Muhammadu ka ba ni dacewa in amsa wa wanda ya yi mini algusa da nasiha,in yi sakayya ga wanda ya ƙaurace mini da kyautatawa,wanda kuma ya yi mini rowa in yi masa kyauta,wanda kuma ya yanke alaƙa da ni in sadar da shi,wanda kuma ya giba ta in ambace shi da alheri,in yi godiya ga kyautataw,in kame daga mummuna.

Ya Allah ni ina mai ba da uzuri game wanda aka zalunta ina hallare a gurin amma ban taimake shi ba.Ko kuma kyautatawa gare ni,da kuma mai munanawa wanda ya ba uzuri amma ban karɓi uzurinsa ba,ko kuma mabukaci da ya bukata daga

[26] Mafatihul Jinan Addu'ar Abi Hamza Aththumaliy

gare ni amma ban fifita zaɓinsa a kan nawa ba,da kuma haƙƙin wani mai haƙƙi da ya zamanto lazimi a kaina amma ban cika musu shi ba,ko kuma aibin wani mumini da ya bayyana a gare ni amma ban suturce shi ba,da kuma duk aikin saɓo da ya fuskanto gare ƙaurace gurin ba.Ya Allah ni ina neman uzuri game da su dukkaninsu da makamantansu,ina mai neman uzuri mai nadama irin nadama mai wa'aztarwa game da abinda ke gaba gare ni da makamantansu".[27]

RAYUWAR IMAMAI:DUNIYA CE MAI FAƊI GAME DA FALALA DA KA'IDOJI

RAYUWAR IMAMAI :TEKU DA KE CIKE DA ILIMI DA SANIN HAKIKA

RAYUWAR IMAMAI:TARIHI NE DA KE CIKE DA JIHADI DA KARAWA DA AIKI SABODA ALLAH.

RAYUWAR IMAMAI:SHAFUKA NE DA KE NA KYAUTA DA BAIWA DA SADAUKARWA.

RAYUWAR IMAMAI TSARI NE CIKAKKE DA KUMA TASWIRA MAI KYAU TA RAYUWAR SAMUM SA'ADA

RAYUWAR IMAMAI MUSULUNCI NE A AIKACE,KA'IDOJI NE A TSARE A RUBUCE.

To amma abin tambaya a nan ita ce ta ita wane abu wannan al'umma ta gano ta binciko game da wanana duniya faffaɗa? Wane gwargwado wannan al'umma ta kamfato daga wannan tekun ilin mai zurfi?Me wannan al'umma ta karanta daga wannan shafuka masu haske?Me wannan al'umma ta amfana da shi na wannan cikakken tsarin da taswirar?

Haƙiƙa abu ne mai matuƙar ɓata rai mutum ya lura da wagegiyar tazara tsakanin zuriyar al'ummar zamani da tarkar da Imamai suka gadarwa al'umma,ka iske ko-oho na ganganci ga wannan taskar mai yawan gaske wadda rayuwar ta tattara a kansu.

Mafi yawancin ɓangarorin mutanen wannan al'umma ba u san kome ba game rayuwar waɗannan manyan jagorori Imamai,waɗanda suka yi ƙoƙarinsu suka yi amfani da dukkan ƙarfinsu suka sadaukar da rayukansu wajen kare addini da fa'idar al'umma.

Gaskiyar al'amarin ita ce,mushkilar samar tazara da nseantarwa tsakanin al'umma da shugabanninta na gaskiya,ba wai yau ta auku ba,abu ne da yake da ya auku

---

[27] Sahifatussajjadiyyah

sakamakon cutar tarihi ce da ta auku tun zamani daban-dabamtsawon da za mu yi ishara ga wasu daga cikinsu kamar haka:-

1. Matsayin shugabanni a tarihi, dangane da su Imamai shugabanni na gaskiya ɗin,waɗanda suka kaance suna yaɗa koyarwa da rubuce-rubuce da goyon bayansu ga tsarin rayuwar shugabanni da salon masu hukuma a tafi da shugabanci.
   A wani ƙaulin muna iya cewa su shugabanni Imamai sun kasance so da yawa su ne masu shugabantar sahun hamayya da bijirewa ga ainihin fanɗarewar da ta auku da al'umma ta kasance a cikinsa tun wancan zamanin.Su ne suka kasance masu nusar da ma'abuta yunƙurin kawo canji a fakaice da shiryar da su abinda za su yi.
   Su ne suka kasance suna jagorantar juyinjuya hali daga gidajensu kuma daga makarantunsu ne aka yi tarbiyyar ma'abuta kawo juyi.
   Saboda haka a bisa ɗabi'a hukuma dole ne ta yi ƙoƙarin mai da su saniyar ware,ta toshe irin tunaninsu daga isa gurin jama'ar al'umma ta kuma sanya wa mabiyansu a kuma yi musa katangar killace su ta hanyar barazana da danniya.
   Alal misali Mu'awiya bin Abi Sufiyan ya yi amfani da duk wata muguwar hanya wajen hana yaɗuwar ambaton sunan Imam Ali binAbi Talib (A.S.) da hadisinsa da falalarsa,haka kuma domin ya ɓata sunan Imam Ali (A.S.) ya ba da umarni na musamman ga dukkan gwamnoninsa yana cewa:-
   "Ku lura ku gani duk wanda hujja ta tabbata cewa yana son Ali da mutanen gidansa to ku share sunansa daga littafin tallafin hukuma,kuma ku hana shi abinda ake ba shi ku hana shi daukiyarsa''.Daga bisani sai ya sake biyar da wani umarnin inda ya ce:-
   "Duk wanda kuka tuhumce da wilaya ga waɗancan mutanen to ku azabtar da shi ku rushe gidansa".[28]
   Mafi muni kuma fiye da duk wannan shi yadda Mu'awiya ya farlanta wa mutane zagin Imam Ali (A.S.) a kan mumbarori da kuma a huɗubobin Juma'a,da addu'o'i har ta zamanto sunna ce da babu makawa kawo ta duk kuma mai huɗubar da ya mance bai yi ba to za a azabtar da shi.[29]

---

[28] Sharhin Nahjul Balagha na Ibin Abil Hadid juzu'i na 3 shafi na 5
[29] Al-Kamil fit Tarikh Juzu'i na 2 shafi na 488

Wannan mummunan cin mutuncin da yaƙin sanarwar a kan Imam Ali (A.S.) ya ci gaba har na tsawon lokaci har zuwa zamanin Umar bin Abdul Aziz wanda shi ne a zamaninsa ya hana zagin Imam Ali (A.S.) bayan an riga an tarbiyyantar da zuriya bayan zuriya a kan ƙiyayya da Imam Ali (A.S.) ta yadda har sunansa ma kawai ya zamanto abin kunya kuma aibu.Wata rana wani matashi wani yaro ya isa fadar Hajjaj bin Yusuf Ath-Thaƙafiy ya ɗaga sautinsa sa'an nan ya ce:- "Ya Amirul muminin iyaye na sun watsar da ni sun sanya mini suna Aliyu.[30]

Sai ambaton sunan ɗaya daga cikin Imaman ko kusantarsa ya zamanto wani abinda mai kiɗimarwa koda kuwa a mafarki ne.

Ya zo daga Al-Fatahu Ibin Shakhufi ya ce:Wata rana idona ya rinjaye ni na yi ririmi har da mafarki sai na ga wasu mutane kusa da ni a mafarki,sai na ce wa wanda ya fi kusa da ni daga cikinsu: wane ne kai? Sai ya ce : daga 'ya'yan Adam.

Ya ce:Sai na ce masa ai dukkaninmu 'ya'yan Adam ne amma abin nufi mene ne ya kawo ka kusa da ni?

Sai ya ce: Ali bin Abi Talib.

Sai na ce masa to kai da kake kusa da shi ba ka tambayarsa?

Sai ya ce:Ina tsoro kada mutane su ce :Ni Rafidhiy ne,wato ɗan Shi'a ne"[31].

Kai hatta daular Abbasawa ma duk da cewa an kafa ne da sunan Ahlul-Bayt(A.S.) kuma sun kasance suna kirari ne da taken Ahlu-Bayt (A.S.) amma da suka gaza shamakance Imamai(A.S.) ko zamowa ɗaya da su a bisa koyarwarsu suka kuma yi hasashen cewa kasantuwar Imamai (A.S.) da yaɗa koyarwarsu hatsari ne ga mulkinsu da su kansu sai suka zage damtse suka yi duk iya ƙoƙarinu wajen yaƙar Ahlul-Bayt (A.S.) da ganin cewa sun shiga tsakaninsu da jama'ar al'umma.

Wata rana ɗaya daga cikin Malaman hadisi a zamanin Mutawakkil Al-Abbasiy mai suna Nasru binul Jahdhamiy ya ruwaito wani hadisi da aka ruwaito daga Manzon Allah(S) cewa: "Ya riƙi hannun Hasan da Husaini (A.S.)kuma ya ce:-

---

[30] Sharhi Nahjul Balagha na Ibin Abil Hadid juzu'i na shafi na 58

[31] Tarikhu Dimasƙ na Abul Kasin Aliyu binul Hasan ibin Hibatullah bin Abdullah bin Asakir juzu'i na 48 shafi na 233 bugu na ɗaya na shekarar 1415 Hijiriyya.

“Duk wanda ya so ni kuma ya so waɗannan biyun da babansu da mamansu to yana tare da ranar Alƙiyama a daraja ɗaya”.Da labari ya isa ga Mutawakkil sai ya sa aka yi masa bulala dubu.’’[32]

Wani mashahurin mai waƙe a zamanin Haruna Rashid Abbasiy,mai suna Mansur Annamiyriy ya kasance yana jin ciwon abinda ake yi wa Ahlul-Bayt (A.S.)na daga gallazawa da cutarwa saboda haka sai ya tsara waƙe yana cewa:-

“Zuriyar Annabi waɗanda son su ne

Ake tsorata tare da a wannan ƙarne

Ake kamun kafa gun Yahudu ko Mishan arne,

Alhali ’yan ummar tawhidi na shamakance su duka.

Sai shi Haruna Rashid ya fusata da wannnan mai waƙe ya aika wani domin ya je ya kashe shi amma sai suka iske gawarsa,sai Haruna Rashid ya ce na yi nufin in zaƙulo harshensa ne ta bayan ƙeyarsa,daga bisani kuma ya so ya sa a tone kabarinsa a ƙone ƙasusuwansa amma sai wasu jama’a suka roƙe shi ya haƙura ya janye yin hakan.[33]

A sakamakon wannan takunkumi na siyasa da na sadarwa ya da hukuma ta tilasta a kan Imamai(A.S.) da yawa daga cikin taskokin da Ahlul-Bayt (A.S.) aka watsar da tarihinsu aka haramta wa al’umma amfanuwa da iyawarsu da isuwarsu yadda ya kamata.

Akwai wani babban al’amari da babu makawa mu yi ishara gare shi a sarari wanda shi ne cewa zalunci da adawa a tarihi da aka nunu wa zuriyar gidan Manzon Allah (S) da nuna ƙyamar su da ware a duk tsawon tarihi da har zuwa yau illarsu da mummunan tasirinsu ke ci gaba duk sun auku ne a sakamakon baƙin jahilci da ra’ayin riƙau saƙandamin kishi da makahon biyayya ga ɓangaranci ko mazhabanci.

Mutum kawai saboda yana bin mazhabar wane a tarihi,wane shi kuma yana ƙiyayya ga Ahlul-Bayt(A.S.) to shi ma sai kawai ya zamanto ya kallafa wa kansa cewa shi ma dole ne ya yi ƙiyayya da Ahlul-Bayt (A.S.).

---

[32] Tarikhu Bagdad na Abubakar Ahmad bin Ali Alkhɗib Al-Bagdadi juzu’i na 13 shafi na 288,bugun Berut na Darul Kutubul Ilmiyya.

[33] .Tarikhu Dimasƙ juzu’i na 13 shafi 69

Ko kuma mutum don kawai ya taso a yankin guri kaza da suke da matsayinsu na musamman game da Ahlul-Byat(A.S.) to shi kawai sai ya ɗauki matsayi irin na wasu ba tare da yin wani nazari ko bincike don tabbatar da gaskiya ba,ko ƙoƙarin al'amari daga wani ɓangaren ba.

Wannan irin ra'ayi kuwa da matsayi kuskure ne ba aiki ne na ilimi ba kuma ba na adalci ba ne,Alƙura'ani mai girma ya kushe irin wannan matsayin da ya aibata Mushirikai masu yin haka inda yake cewa:-

"Haka nan kafin kai ba Mu aika wata Alƙariya mai  wa'azi ba har sai majiya daɗinsu sun ce ai mu lalle mun sami iyayenmu a kan al'umma kuma mu masu koyi ne a kan matafiyarsu.Ya ce shin koda ma na zo muku da mafi shiriya fiye da wanda kuka sami iyayen naku a kai,suka ce mu haƙiƙa masu kafircwa ne da abinda aka aiko ku da shi".(Surar Zukhruf aya ta 23-24)

Abinda ya kamata ga Musulmi wayayye mai fahimta, musamman ma matasa; shi ne, ya raba kansa da ra'ayin riƙau da makahuwar biyayya,kuma ya yi nazarin tarihi daki-daki a kowane  ɓangare, domin ya gano abinda Ahlul-Bayt(A.S.) suka gadarwa al'umma saboda ya san abubuwan gaskiya da haƙiƙa da ke ƙunshe a ciki da mafifutan ra'ayoyi da maɗaukakan manufofi har ya kai ga sanin gaskiya.

2. Koƙarin 'yan mulkin mallaka, babu wani da yake shakkun cewa musulmai sun mallaki yankin muhalli da yake da muhimmanci da kuma tarin dukiya mai tsananin yawa waɗanda suka sanya mu zamanto sun jawo mana hankali da manufar 'yan mulkin mallaka, har ila yau mun san cewa 'yan mulkin mallaka na amfani da dukkan wata hanya, ba wai kawai ƙarfin soja ba,har da rubuce-rubuce da furofaganda a kanmu;saboda haka babu makawa mu fahimci dabarar 'yan mulkin mallaka da suke amfani da shi don su tabbata sun shiga tsakanin matasanmu da tarihin magabatansu da koyarwarsu da matsayinsu.

Sukan yi amfani da alƙaluman ma'abuta son rai da jahilai,wajen rikitar da mutane game da shugabannin Musulunci masu daraja da al'amuran da suka auku a tarihi da rusawa daraunanawa ga ainihin darajar nagari a maye gurbinsu da miyagu fanɗarrru.

Daga cikin irin wannan mummunar hanyar gurɓata haƙiƙar da cuɗanya ƙarya da gaskiya akwai littafin wani mai suna Ibrahim Jabhani ya rubuta na

munanawa ga Imam Ja'afrus Sadiƙ(A.S.), da wani kuma da aka fito da shi mai suna "Sanin Haƙiƙa game da Amirul Muminina Yazid ɗan Mu'awiya" da kuma wani littafin da ke kariya ga 'Hajjaj bin Yususfuth-Thaƙafiy".

Wannan aikin yana da wata manufa mai hatsarin gaske,wadda ita dawo yanayin ƙayayya da gaba a tsakanin musulman wannan zamanin ta hanyar dawo musu da tarihin rikice-rikicen da suka yi ta aukuwa a da can domin a shagaltar da su a tayar musu da fitintunu su gaza ci gaba su kasa warware matsalolinsu na yanzu da suke ci musu tuwo a ƙwarya.

Hanyar magancewa da fuskantar wannan makircin na 'yan mulkin mallaka shi ne ta hanyar aiki da hankali da tunani a kan al'amari tare da neman gaskiya duk inda take tare da duk wanda take ba tare da tayar da fitinar ɓangaranci ba ko nuna son rai ba.

3.Mummunar fahimta dangane da rayuwar Imamai(A.S.),kowace zuriya tana rubuta tarihinta da mahanga ta musamman irin ta zamaninta da al'amuran da ke aukuwa tunda yake zamanin da sun rayu cikin koma baya narkewa da daskarewa ,mahangarsu kuma ta tafi ne tare da ke aukuwa a zamantakewarsu to da suka rubuta tarihin Imamai sai yanayin ya yi tasiri a kan rubutun nasu.

Saboda kasancewar zuriyar wancan zamanin sun sallama wa tsoro da miƙa wuya da yin shiru dangane da zalunci don haka suka yi ta ƙoƙarin dalilai da hujjojin yarda da amincewa da wancan yanayin ƙasƙancin da yarda da zalunci.

Saboda su zuriyar wancan zamani sun ware kansu daga fagen rayuwar al'umma sai suka takaita da fassarar abubuwan da ke aukuwa a rayuwa fassarar 'yan kallo kawai ba tare da sun ba da wata gudummawa ba wajen samar da abinda ke aukuwa,suka yi fassara irin ta kintatawa da ƙaddarawa da irada suka shigo cikin ala'amuranrayuwar ɗan Adam.Wato ;Iradar Allah ita ce ta karya daular Banu Umayya ba yunƙurin Alawiyyawa ba ko juyin juya halinsu.

Kudurar Allah ita ce ta ɗora Abbasawa a ka karagar mulki ba ƙulle-ƙullensu da dabarunsu ba ko goyon bayan jama'a ba.

Saboda haka nufin Allah shi ne ya sa Imamai suka kasance cikin takurawa da azabtarwa da kora ba wai fafatawarsu game da zaluncin azzalumai ba ya haifar da haka ba.

Ta haka tarihin rayuwar Imamai ya iso da wannan irin fassara ta kuskure wanda ke mai da hankali a kan wahalhalun da suka sha da kuma karamominsu da suka saɓa wa al'ada,amma dangane da fafatawarsu ta siyasa da gudummawarsu a zamantakewa, da gudummawarsu ta fannin ilimi wannan ba abu ne mai muhimmanci da za a himmatu da shi ba.

Saboda haka a wannan zamanin muna da matsananciyar bukatar sanin rayuwar Imamai a halinta mai haskakawa,da dukkan fannoninsa mai annuri da dukkan ɓangarorinsa mai amfanarwa.

ADIRESHIN MARUBUCI

Kasar Saudiyya

P.O.Box 1322 Qateef 31911

Phone number +966138555210

Fax number+966138512600

Internet :www.saffar.org

Email:office@saffar.org